# KIRISTANCI--ADDINI MAI IKO

# CHRISTIANITY--A RELIGION OF POWER

**KOS NA FASTOCIN CRCN**

**Course Prepared for the Pastors**
**Of the Christian Reformed Church of Nigeria**

**Takum, Watan Satumba/September, 1993**

**MAI TANAJIN KOS**
**Author of the Course**

**DR. JAN H. BOER**

**ABUBUWAN DA KE CIKIN KOS**
**KIRISTANCI--ADDINI MAI IKO**
**GABATARWA**

**A. Musulmi**
**B. Matsafa**
**C. Karisimatikai**

**IKO CIKIN LITTAFI MAI TSARKI (LMT)**
**IKO WAJEN TURAWAN MISHAN**

**A. Tushen Kimiyya da Umarnin Ingantar da Halitta (Cultural Mandate)**
1. **Zamanin Halitta**
2. **Fadadden Dan Adam Mai Zunubi**
3. **Zamanin Ceto**

**B. Kimiyya da Biyuntaka**

**C. Kimiyya da Biyuntaka da Jiyya**
1. **Asalin Jiyya ta Zamani**
2. **Damuwar Jiyya ta Zamani**

**IKON AIKATA MA'UJIZAN**

**A. Shaidar LMT**

**B. Shaidar Tarihin Ikiliziya**
1. **Zamanin Ubanni**
2. **Zamanin Tsakiya**
3. **Zamanin Gyaran Ikiliziya (1500-1900)**
4. **Zamaninmu na Yau**

**C. Shaidar Marasa Bi**
**D. Shaidar Refom**

**CRCN--INA ZA MU?**

**LITTATTAFAI**

**GABATARWA**

**Kun yarda cewa Kiristanci--addini ne mai iko?**

**In "I"-- a bayyana dalilin da aka yarda. Kawo misalin ikon.**

**In "Babu"-- In ji wa? Domme? Misali?**

## A. MUSULMI KE CEWA:

**Kiristanci sha'anin ruhu ne kurum, na ikilisiya ne. Ba ta da taimakon ginin kasa. Ba na duniya ba ne, sai sama. Amma Musulunci tana da taimako da yawa game da siyasa da kasuwanci da sauran harkokin duniya. Musulunci is a way of life. Ta shafi kowace fannin rayuwarmu a duniya. Ba inda Musulunci ba ta da magana ko hikima ko koyarwa. Wannan musamman zargi ne na marigayi Shaikh Abubukar Gumi. GASKIYA CE KUWA?**

## B. MATSAFA

**Wani lokaci sai ka ce Matsafa ke da iko fiye da Kirista. Sukan aikata abubuwan da Kirista ba su iya ba ko kuwa kawai ba swa yi. Kawo misali. Me ya sa Kirista ke zuwa manyan matsafa a lokacin matsi? Me ya sa Kirista ke zuwa matsafa bayan da aka salame su daga asibitin Kirista, wai sun warke?**

**Wannan damuwa ba a nan Nijeriya kadai ba. Paul Hiebert, wani mishan a kasar India a da, shi ma yana maganar wannan batun. Ko a kasar India ma Kirista suna so su danganta ga jiyya ta zamani tare da musun kasancewar ruhohi. Duk da haka dai a lokacin ciwo ko wani matsi sukan nemi taimako wajen masu jiyya ta gargajiya iri tasu wato na addinin Hindu ke nan. Daidai da Nijeriya. ME YA KAWO HAKA?**

## C. KARISIMATAKAI (Charismatics)

**Wadannan Kirista ne; 'yan'uwanmu ne, amma wadansunsu ke zargin membobin TEKAN da wasu darikai kamar su Anglican da Baftist da sauransu. Wai ba mu da ikon warkaswa sai tare da magani, ba mu da ikon magana cikin harsuna da dai sauransu. Wato, ba mu da iko ke nan. Bisharármu mara iko ne da mara karfi. In ji matasanmu masu yawa, sun fi son koyarwar Karisimatikai da ayyukansu da na CRCN da na sauran darikan TEKAN domin wai ba mu da iko kuma ba murna cikin sujadarmu. KO GASKIYARSU? ME KA GANI? A TUNA FA--RAN WANKA BA A BOYE CIBIYA!**

**IKO CIKIN LITTAFI MAI TSARKI**

**A duba takarda inda aka kwashe dukkan ayoyin LMT wadanda ke maganar iko. In ka bincika su ayoyin sai ka gani iko iri-iri ne, amma tushen dukkan iko shi ne Ubangiji Madaukaki da kansa. Shi Mai Iko dukka, wato Uba da na Da da na RMT. Sauran ikoki ke karkashensa. Ba su da tushen kansu. Ubangiji Allah ke bayarwa da karba (Ayuba 1:21).**

**A. Ikon Allah**

**Na yi kokari in raba zancen ikon Allah da ikon Yesu Kiristi da kuma da ikon RMT. Za a iya raba su cikin wasu ayoyi, amma cikin ayoyi da yawa da kyar za a ce ana maganar ko ikon Allah ko na Da ko na RMT. Saboda haka ban raba su ba.**

**B. Ikon Kirista**

**C. Ikon Shaidan da na Rundunarsa**

**D. Ikon Marasa Bi**

**E. Ikon Halitta**

**F. Ikon Masu Sarauta**

**IKO WAJEN TURAWAN MISHAN**

**Sai mu duba da kyau. Ko ka taba ji Turawan Mishan ke maganar iko ko suka yi aiki da shi? Ikon da ni ke magana shi ne iri na Yesu da na masu bi a cikin SA.**

**Idan ka gani ko ka ji suna maganar iko, ka bayyana abin da ka gani ko ji.**

**Wane irin iko ne suka nuna?**

**Im ba ka gani ba, me ya sa ba alamar iko a wajensu?**

**++++++++++++++++++**

**ABIN LURA: Ni mai magana ban ware kaina daga cikin kungiyar Mishan ba. Duk abin da na kawo cikin kos din nan, wato karfinsu da rashin karfinsu, ya shafe ni, ni ma.**

**+++++++++++++++++++**

**Mishan sun zo ne da maganin Turawa da asibitoci.  A wurin ne sukan yi aikin jiyya. Ko shi ne ikon da LMT ke magana?  Ina dangantakar jiyya na zamani da jiyya cikin LMT?  Me ya hada su?**

**Wasu Karismatikai sukan rena jiyya iri ta zamani, cewa dabarar dan adam ne kurum. Ba ruwan Allah da irin wannan jiyya. Ba na Ruhu ba ne.  Ba na Yesu ba.  Hikimar duniya ce kurum.  HAKA KUWA?  ME KA GANI?**

## A.  TUSHEN KIMIYYA DA UMARNIN INGANTAR DA HALITTA (CULTURAL MANDATE)

**Don mu san amsa ga wadannan tambayoyi ya kamata mu san tushen kimiya. Kimiya ce ta kawo mana jiyya iri ta Mishan.**

### 1.  HALITTA

**Wane umarni ne Ubangiji ya aza ma dan adam tun farko? Duba Far. 1:26-28.  Da Turanci ana ce da umarnin nan Cultural Mandate. Da Hausa sai mu yi amfani da "Umarnin Ingantar da Halitta" (UIH).  Ikilisiyar Reformed takan dauki UIH tushen zaman dan adam a duniya.  Ubangiji ya ce mu fitar da asirin da ke a boye cikin halittarsa, asiran da Shi Kansa ya boye su ciki.  Mu ingantar da halittarsa, mu yi amfani da dukan abubuwan da Shi Mahalicci ya yi. Mu yi mulkin halittar ke nan.**

**Farkon mulkin kakaninmu kan dabbobi (kifaye, tsuntsaye, da sauransu) da kuma kan tsirace-tsirace da dukan itatuwa (Far. 1:28-30).  Wadannan sun zama masu abinci ke nan.  Yana moronsu. Sai kuma cikin Far. 2:19-20 Adamu ya rada ma kowace dabba sunansa. Ba wai dabbobin gida kawai ba fa, amma har na daji.  Dabbobin da muke jin tsoronsu yanzu, muna gudunsu, shi Adamu ya na mulkinsu, yana rada masu sunayensu.  Ga kuma yadda Ubangiji ya sa kakaninmu su yi noma, su kiyaye Gonar Aidan (Far. 2:15).**

### 2.  FADADDEN DAN ADAM MAI ZUNUBI

**Ko da yake dan adam ya fadi cikin zunubi, bai rabu da halinsa na mutumtakarsa ba.  Ya cigaba da aikinsa, wato ingantar da halitta.  Duba irin sabobbin abubuwan da ya kera.  Kayinu ya gina birni. Yabal ya shirya alfarwa (tents). Yubal ya bullo da giraya da sarewa.  Zulai kuwa ya kera tagulla da bakin karfe   (Far. 4:17-22).  Har yanzu dan adam ke taunan asirin halitta kamar yadda Ubangiji ya halicce shi.  Amma yanzu yana yi don kansa, ba domin ya bauta Ubangiji cikin duniya ba.  Kayinu ya kashe dan'uwansa. Lamek ya zama mai fahariya; ya mai da kansa kamar ya fi Allah wayo.**

Mugunta yaduwa kawai take yi ko'ina har Ubangiji ya ga muguntar ta kasaita a duniya kuma dukan zace-zacen  tunanin zuciycar mutum mugunta ne kullayaumin (Far. 6:5).  Allah ya ja kunnen dan adam da ruwan tufana, amma duba irin ayyukan da Nuhu ya yi daga baya. Ya bugu. Ya kuma kwana da yaransa 'yan mata.

Bayan da girman kai na dan adam ya cika da ginin hasumiyar Babila, Ubangiji ya warwatsad da 'yan adam har ya dagulla harshensu. Amma ginin hasumiyar dai ya nuna karin mulki da karin ilimi.  Komai muguntarsa, dan adam zai yi mulkin duniya don kuwa halittaccen halinsa ne.  Ya zama masa dole ne.  Kamar kyanwa ba ta iya rabu da farauta ba, haka dan adam ba zai iya dena mulkin halitta ba.

Mulkin halitta aka cigaba da shi, amma cikin mugunta ne.  Daga baya yawancin abubuwan da aka kera kayayyakin yaki ne domin kisan kai.  Ko in aka kera wani abin kirki, za a yi amfani da shi domin girmama dan mutum, ba Allah ba.  Kuma aka kera su ne domin a zalunci.  Hikima ta karu, amma sai tare da girman kai da fahariya.

Akwai wani shehun malamin Refom mai suna ABRAHAM KUYPER (1837-1920) wanda ya kafa jami'a inda na sami digiri nawa, wanda kuma aka takaita ayyukansa cikin littafinsa da na juya zuwa Turanci, wato YOU CAN DO GREATER THINGS THAN CHRIST.  Cikin CRC a Kanada da Amirika da kyar za ka sami mai tauhidin da ya fi Kuyper tasiri. Haka ma cikin kasar The Netherlands inda aka haife shi, kasar asalin CRC da na yawancin membobinta, kasa inda aka haife ni mai shirin kos din nan. Dalilin da mu a CRCN ba mu san shi sosai ba biyu ne.  Na daya shi ne ya wallafa littattafansa cikin yaren Dutch wanda masu Turanci ba swa ji.  Na biyu, yawancin membobin CRC masu saurare shi ba swa fita su yi aikin mishan a waje. Yawancin mishanaran CRC da shugabannansu ba su damu da shi sosai ba. Sun fi sauraron mutane na waje wadanda ake ce da su "Evanjelikai" (Evangelicals).

To, shi Kuyper din nan ya bayyana mamu yadda bayan faduwarsa, ikon dan adam kan halitta ya soma raguwa.  Maimakon dabbobi su yi masa biyayya, ya soma jin tsoronsu.  Ba swa yi masa biyayya yanzu.  Maimakon ya tone asirin da ke cikin duwatsu, dan adam ke jin tsoron duwatsu domin ya yiwu akwai wasu iskoki ko ruhohi iri-iri a samansa.  Maimakon ya mori itace, yana yi masu hadaya. Har yanzu ma dan adam mai zunubi yana jin tsoron abubuwan da ke faruwa.  In yana kasa, ya na jin tsoron hadari da iska. In yana teku ya na jin tsoron zurfin ruwa da rakuman ruwa.  In yana jirgin sama yana jin tsoron faduwa.  In yana jeji yana jin tsoron bata hanya da dabbobin daji.  Da kuma ko'ina yake ya firgita saboda iskoki da ruhuhi da ikoki da maita da dai sauran abubuwa masu firgitard da dan adam. Wato kullum sai jin tsoron halitta ya ke yi.

Sha'anin dan adam bai bace wajen halitta (nature) kawai ba, amma har tsakaninsa da makwabcinsa. Ya cika da zalunci da girman kai da tsoro duka gaba daya.  Ko inda ilimi ya yi zurfi, sai tare da zalunci.  Inda dukiya ya karu, sai a hannun mutane kima.  Wasu sukan ci jikunan 'yan'uwansu.  Wasu sukan bizne mata masu yawa sa'anda za a yi ma sarki jana'izu. Wasu sukan yi ma gumakunsu hadaya da yaransu.

Mutum wanda Ubangiji ya sarautad da shi ya zama bawa mai jin tsoro.  Kusan a ce ba sauran mulki gareshi, ba sauran darajarsa.

## 3.   ZAMANIN CETO

Yesu ya zo ne don ceton halitta gaba daya, ba domin dan adam kawai ba. Duba musamman Kol. 1:13, 15-20 da kuma Ibr. 2:7-10. Ya zo ne domin gyaran tsohon fadaddiyar halitta, ya sabonta ta, ta sake amsa manufar Ubangiji ta asali, wato halinta na farkon halitta. Ya kuma yi ma almajiransa wasu manyan alkawarai. Ga Yah. 16:13--"Sa'ad da kuwa Ruhu na gaskiya ya zo, zai bishe ku cikin dukan gaskiya." Ga kuma Yah. 14:12 inda Yesu ya ce, "Lalle hakika, ina gaya muku, duk wanda ke gaskatawa da ni, ayyukan da nake yi, shi ma haka zai yi. Har ma zai yi ayyukan da suka fi wadannan." Har yanzu ma Ubangiji ya ba almajiransa ikon fitar da aljannu da sauran ayyukan al'ajibi domin su yi aiki da ikon ba a zamanin da suke tare kawai ba, amma har bayan da ya hau sama. (Duba jerin ayoyi na game da zancen iko.)

A yi ayyukan da suka fi na Yesu? Da ka wani Kirista yana fada wannan da za ka tsauta masa kwarai. Wane shi da zai yi magana haka. Na juye wani Littafin Kuyper daga Turanci mai suna . Kwanan baya wasu bishops guda biyu na Ikiliziyar Roma sun ga takardar Kuyper, YOU CAN DO GREATER THINGS THAN CHRIST, wato KA IYA AIKATA ABUBUWAN DA SUKA FI NA YESU, kan wani tebur. Daya ya nuna ma abokin aikinsa, sun karanta sunan littafin har ma sun kada kansu. Sunan bai gamshe su ba. Ai, na gane da damuwarsu. Ya yiwu a ce maganar bidi'a ce. Sai dai Yesu da kansa ya fada. Ba inda za a ki zancen.

Maimakon a kyale wannan zancen Mai Cetonmu ya kamata mu gwada kanmu. Wane ne ke aikata fiye da Shi? A ina ne ake yin wannan? A yaushe ne Yesu Ya fara cika wannan alkwarin din nan? Akwai darika wadda take aiki da alkwarin kuwa?

Wadansu sun dauka cewa sune 'yan alkawarin nan da shi ke suna warkar da marasa lafiya da addu'a da sa hannu daidai da yadda Yesu ya yi. Wato su Karismatikai ke nan. INA AMSARMU? Gaskiya ce kuwa ko babu? Ina dalilin amsarka?

Kuyper ya amsa cewa ya yarda amma kuma bai yarda ba. A wani bangari ya yarda. Za mu dawo wannan zancen nan gaba. Amma a wani bangari kuma ya ki domin a ganinsa wadannan mutane ba su san zurfin ma'anar zancen da Yesu ya yi ba. Ko wadanda suke warkar da mutane ta wajen addu'a ba magani, ba inda za a ce ayyuka nasu sun fi na Yesu. Mai yiwuwa ne a ce nasu daidai da na Yesu amma bai wuce haka ba.

Duk da haka akwai inda Ubangiji ya cika alkawarinsa wajen dan adam, wato a fuskar kimiyya. Wadansu sun dauka sai ka ce kimiyya dabam, addini dabam. Ba abin da zai hada su. Kimiyya sha'anin jiki ne, sha'anin duniya; addini kuwa na ruhu ne. Saboda haka su Karismatikai ba ruwansu da kimiyya, ba ruwansu kuma da maganin da aka kera ta wajen kimiyya, ba ruwansu da asibiti. Ba na Allah ba ne.

Amma Kuyper ya amsa cewa kimiyya ta fita ne daga zuciyar dan adam wanda aka yi masa sabuwar haifuwa, dan adam wanda ya bada gaskiya ga Yesu Kiristi. Da ikiliziya ta kafu sosai a Turai, balle a bayan Reformation, wato Gyaran Ikiliziyar da aka yi a zamanin Luther da Yohanna Kalvin, suka rabu da tsoron halitta. Kuma Umarnin Himmantar da Halitta ya shiga zukatansu. Sun gane cewa bai kamata su ji tsoron halitta ba, amma su yi mulkinta, su tone asirinta su more su asiran domin ingantar matsayin dan adam a duniya. Wani mutum mai suna Francis Bacon, haifaffen kasar Ingila (1561-1626), yana cikin wadanda suka soma aikin kimiyya. A kasa kunne ga shaidarsa cewa kimiyya hanya ce ta bauta ma 'yan adam. Umarnin Himmantar da Halitta shi ne tushen kimiyyar. Kimiyya kyauta ce ta ceton da Ubangiji ya yi mamu ta wajen ya 'yantad da mu daga bautar halitta da jin tsoronta. Ta wajen kimiyya dan adam

ke aikata abubuwa iri-iri har ma abubuwan da ake yi yanzu masu ban mamaki ne kurum. Ta hanyar kimiyya muna aikata abubuwan da ko shi Yesu ma bai yi ba. Ta hanyar kimiyya Ubangiji ya bishe mu cikin gaskiya, ya cika alkwarinsa na Yah. 14:12.

Wato tushen kimiyya da farkonta na Ruhun Allah ne a zuciyar masu bada gaskiya. Sai dai daga baya ko marasa bangaskiya su ma sun koya. A yanzu haka a zamaninmu na yau ake samun masu kimiyya a kowane addini, ba Kirista kawai ba. Yawancin mutane ba su san tarihin abin ba. Kuma da shi ke kimiyya ta kawo mamu abubuwa iri-iri ne, yanzu tana da daraja fiye da addini wajen mutane da yawa. Yanzu ana cewa babu gaskiya sai dai ta hanyar kimiyya. Kimiyya tana aiki da abin da ake gani, ake tabawa, ake aunawa. To sha'anin ruhu dai mara ganuwa, mara tabawa ne, kuma ba a auna shi. Saboda haka an fi son kimiyya da addini. Kimiyya ke da daraja fiye da addini wajen mutane iri-iri.

Wato da shi ke yanzu mutane da dama ba su gane da dangantakar Kristanci da kimiyya ba, ana mai da kimiyya kamar ba ruwan Allah, ba dangantakarta da addini (secularism). Bugu da kari, da shi ke mutane da dama sun rena addini har ma sun ce, da shi ke kimiyya ba ta nuna akwai Allah ba, to ba Allah ke nan kurum! Shi ne daya daga cikin dalilan da Karisimatikai sun mai da kimiyya sha'anin duniya ne kurum, ba abin da ya hada ta da Ruhu.

## B. KIMIYYA DA BIYUNTAKA (DUALISM)

Ku wadanda kuka taba karatun littattafaina ko kuwa kun taba jin jawaban da nike yi cikin tarurruka dabam dabam za ku tuna da wannan sabon Hausan da na kaga, wato BIYUNTAKA ko kuwa DUALISM. Wannan biyuntaka tushen dalili ne da mu Kirista ba mu tashi tsaye a Nijeriya ba, in ji CAN. Na takaita ma'anar biyuntaka cikin dan takarda mai suna CHRISTIANS AND MOBILIZATION (shafi 11-12). Masu goyon bayan biyuntaka suna cewa wai

1. Halitta ta rabu kashe biyu, wato ga na jiki ko kuwa na duniya da kuma ga na ruhu. Su dabam ne. Ba su hadu ba ko da ya ke an same su cikin mutum.
2. Ubangiji Allah ya fi son ruhu da jiki. Saboda haka in za ka yi aikin Ubangiji sai ka kyale sha'anin jiki, ka mai da hankali ga na ruhu kadai.
3. In kana neman ganewa na game da sha'anin ruhu, sai ka karanta LMT. Amma in kana so ka san wani abu game da batun duniya dai, sai ka kyale LMT, ka yi amfani da tunanin dan adam kadai (human reason). A nan LMT ba zai taimake ka ba.

Ikiliziyar Roma ta shirya wannan koyarwar biyuntaka har ba za ka gane da koyarwarsu ba im ba ka san asirin wannan ba. Cikin masu gyaran Ikiliziya akwai wadanda suka ki biyuntakar din nan, amma ba ta sharu daga cikin Gyararriyyar Ikiliziya (Protestant) gaba daya ba. Kalvin yana so ya ki biyuntakar, amma in ka karanta littattafansa za ka gani bai rabu da ita duka ba. Luther ya rungume biyuntakar gaba daya. Ko da yake Ikiliziyar Refom ba ta son biyuntaka, tana zuciyar wasu mishionarai nasu har suka kafa ikiliziya da wannan ra'ayin.

**Ko da yake masu kimiyya na farko sun hada kimiyyarsu da zancen addini kamar shi Francis Bacon din nan, daga baya aka soma aiki da biyuntaka. Ana cewa addini na ruhu ne. Yana bukatar a yi aikinsa tare da LMT. Amma masu kimiyya sai da jiki; LMT bai shafe ta ba. Addini dabam, kimiyya dabam.**

## C. KIMIYYA DA BIYUNTAKA DA JIYYA TA ZAMANI

### 1. ASALIN JIYYA TA ZAMANI

**Da aka soma ganin amfanin kimiyya aka fara moron hanyar aikinsa ta kowane fanni har ma cikin jiyyar da aka yi ma dan adam mara lafiya. Hanyar kimiyya ke nan an zabi wani abin da za a tone asirinsa, a san abin da ke ciki da kuma amfaninsa. Misalin itace. Wanda ya na so ya tattauna itace zai raba itacen kashe-kashe. Zai yanka katako ya auna karfinsa da kuma dalilin layi-layi da ake samu a katako. Zai yanka bawonsa ya ga halinsa. Zai tone saiwoyin a kasa ya gane yadda suke jan ruwa. Zai cire ganye ya yayyanka har da fure.**

**Haka aka soma yi da jikin dan adam. Da farko aka mai da jikin mutum abu ne wanda ba za a taba ba, amma wani Baturen kasar Farans (France) mai suna Rene Descartes (1596-1650) ya kawo zancen biyuntaka cikin jiyyar dan adam. Ya ce kada likita ya damu da ruhun mutum; ruhunsa sha'anin addini ne, ba ruwansa da jiyya. Ya ce masu jiyya sai su bincika jikin mutum daidai yadda akan tattauna sauran abubuwan halitta. Ba wani bambancin jikin dan adam da sauran halitta. Idan mutum ya gamu da ciwo sai a tattauna jikinsa, a san inda ciwon ya ke. In zuciya ne, sai a kawo maganin zuciya ko kuwa a yi masa aiki. In hanta ne, haka ma za a yi. Wato jikin mutum kamar injun ne wanda za a iya gyara sashin da ya lalace. In ya gyaru, shi ke nan, mutumin ya warke! Ba sauran damuwa.**

**Hanyar jiyyar nan ya kawo taimako kwarai da gaske. Dukanmu mun tuna da taimakon da da muka samuwa a tsohon asibitocin mishan. Kimiyya kyautar Allah ce. Jiyya iri na kimiyya ko kuwa na zamani kuma yana iya warkar da cututtuka iri-iri wadanda da za su kashe mutum. Ba shakka mun gode da jiyya iri na zamani. To, shi ne irin jiyyar da mishan suka gabatar mamu da ita a nan kasar Nijeriya.**

### 2. DAMUWAR JIYYA TA ZAMANI

**Ko da yaka mun mai da jiyya ta zamani hanya ce mai albarka, akwai damuwa, babbar damuwa ce mai muhamminci kwarai. Damuwarta ita ce masu jiyya irin wannan ba su mai da hankali ga wasu abubuwa wadanda suka kawo ciwo ko kuwa wadanda suka kara zafin ciwon in ba na jiki ba. Ba su damu da wani ciwo ba im ba su ga tushensa cikin jiki ba. Ba wuya su ce ba ka da ciwo! Domin ba su ga wani abin da ya lalace a injun naka ba, wato jikinka.**

**Wato sun san dalilin ciwo guda kawai, wato wani sashin injun naka ya lalace. Amma dalilan ciwo sun fi haka. Akwai abubuwa iri-irin da suka kawo mamu rashin lafiya. Mai yiwuwa ne akwai ciwo a jikinka, amma tushensa ba jiki ba. Kana da damuwa ne**

saboda sha'aninka da Allah ba daidai ba, dangantakarka da matarka da wuya, ba ka da aiki har ma yaranka ke jin yungwa, ba ka share gidanka ba har ya yi datti, mulkin gwamnati yana iya kawo damuwar. In mai jiyya bai nemi tushen ciwon ba, ai, an yi aikin sama-same ne kurum.

Bugu da kari masu jiyya na zamani sukan kyale abubuwan da ke damumnu a nan Afirka. Idan wani abu yi bace a jikina, wa ya yi mini? Kuma ina dalilin? Da shi ke kimiyya ba ta damu da abubuwa mara ganuwa ko mara tabuwa ga, jiyya ta kimiyya kuma ba ta damu da irin wadannan tambayoyi ba. Da shi ke masu jiyya ba su da amsa, mutanenmu, bayan da aka sallame su daga asibiti, sai su je gun matsafa don su san tushen abin. Kuma idan sun ga damuwar mutum ta ruhunsa ce, za su ce wannan ba nasu ba, su tura mutumin gun fasta. Wato duk aikinsu ya kafu ne kan ginshikar biyuntaka. Har yanzu ma yawancin likitoci na jiyyar zamani suna fahariyar maganinsu fiye da misali, sun rena kowace hanyar jiyya ban da nasu, balle maganin gargajiya tamu a nan Afirka. Renin nan kuwa babban kuskure ne da shi ke an sani cewa su likitocin gagarjiya sukan warkar da ciwoce-ciwoce da yawa wadanda sukan fi karfin jiyyar zamani.

Ko da yaka jiyyar zamani tana da amfani kwarai da gaske ba ta biya mamu dukan bukata ba. Shi na ya sa na kafa wani kungiyar Wholistic Health Care, wato hanyar jiyya wadda za ta tattauna curuta a kowace fuska, ba fuskar jiki kadai ba. Da kuma dole ne jiyyar irin wannan ta kasa da shi ke aka gina ta bisa ginshiken biyuntaka.

Abin tausayi ne yadda su mishan ba su gane da damuwa jiyya iri tasu ba. Sun dauke ta kyauta ce daga wurin Allah da kuma hake ya ke. Amma ba su gane da babban kuskuren biyuntaka ba da shi ke ta riga ta rinjayi zukatansu. Renin maganin gargajiya ma abin mamaki ne. Sai ke ce ba su san tushen addinin Kiristanci ba wanda ya koya mamu cewa Ubangiji yana tare da dukan kabilun duniya. Komai duhun addininsu da na al'adunsu, ba a rasa hasken Ubangiji a ciki ba (doctrine of common grace). Saboda haka, maimakon a ki na gargajiya da ganga sai a tattauna a nemi gaskiyar da ke ciki a yi amfani da ita. Wato ba su san kuskure na nasu hanyar ba kuma ba su gane da hasken Ubangiji kan Afirka ba. Abin mamaki ne kwarai da gaske. Kuma abin tausayi ne domin wannan halin ya kawo mamu damuwa ba kadan ba.

Abin da muka samu yanzu shi ne kimiyya kyautar Allah ce na ceto. Ta wajen jiyyar kimiya ana warkar da mutane fiye da yadda Yesu ya yi. An cika alkawarinsa na Yah. 14:12. Ta wajen jiyyar kimiya kuma ana cika Umarnin Ingantar da Halitta. Amma albarkar ta zo ne garwaye da duhun biyuntaka. Kimiyya wani iko ne wanda Ubangiji da kansa ya bayar. Wadanda suke raba kimiyya da sha'anin ruhu ba su san abin da suke yi ba. Kin jiyyar kimiyya yadda Karisimatikai suke yi babban laifi ne, reni ne ga kyautar Allah da cetonsa.

## IKON AIKATA MU'UJIZAN WARKASWA

To, yanzu mun kai goshin wata babbar tambaya. Wato babu warkaswar da mu Kirista za mu yarda da ita sai ta wajen jiyyar kimiyya? Me za mu yi da mu'ujizan da muke jin labarinsu cikin LMT? Lokacinsu ya wuce ne? Ikon aikatansu ya kare ne?

Ra'ayi ya rabu biyu ne. Yawancin Turawa sun mai da zancen mu'ujiza jahilci ne da rudi. Wadansu Turawan Kirista suna cewa ko mu'ujizan da ake jin labarinsu cikin LMT

**tatsuniyoyi ne kurum, ba su faru ba. Wasu Turawan Kirista sun yi na'am da mu'ujizan da ke cikin LMT, amma ba su yarda cewa ana aikata mu'ujiza har wa yau ba. Wai lokacinsa ya wuce. Ba bukatarsa yanzu. Amma a Afirka da sauran kasashe akan aikata mu'ujizai iri-iri wandanda masu kimiya ba su iya su gane da su ba. Ga wasu ayyuka masu ban mamakin da wadansu manyan matsafa sukan yi. Ga wasu ayyukan da mutanen India masu addini dabam dabam suke yi. Ga kuma warkaswar da wasu Karisimatikai suke yi. ME ZA MU CE? WADANNAN DUK RUDI NE? DUK AIKIN SHAIDAN NE? LOKACI YA YI MU TATTAUNA ZANCEN NAN DA ZURFI YANZU.**

## A. SHAIDAR LMT

**Dukanmu masanan LMT ne. Mun riga muka san labarin dukkan mu'ujizan cikin LMT. Mun san na Annabi Musa. Mun san na Annabi Iliya da na Elisha. Ga kuma da yawa bi da bi na Macecinmu Isa Almasihu. Na karshe kuma ga mu'ujizan da Manzanni suka aikata a loton da suke tare da Ubangiji da kuma daga baya cikin littafin Ayyukan Manzanni.**

**Amma fa sai a duba da kyau. Ba mabiyan Ubangiji kadai ke aikata mu'ujizai ba. Mutane iri-iri ke da ikon aikata abubuwan da kimiyya ba ta iya gane da su ba. Shi ne ya sa masu kimiyya sukan mai da su rudi ne kurum. Ga masu sihiri wadanda ke a fadar Fir'auna (Fit. 7:11-12, 22; 8:7). Ga kuma wasu masu koron aljannu (Markus 9:38-40; Luka 9:49-50). Har yanzu ga mai sihiri Saminu (A.M. 8:9-13; 18-24).**

## B. SHAIDAR TARIHIN IKILIZIYA

**Akan raba tarihin ikiliziya cikin wasu zamanai. To, akan ce da zamani daga shekara 100 zuwa 600 Zamanin Ubanni (Patristic Era; Church Fathers).**

### 1. ZAMANIN UBANNI

**A zamanin akwai wasu manyan shugabannin da suka shaida a rubuce cewa a zamaninsa masu bi suke da ikon mu'ujizai, balle ne warkaswa. Wani mai suna JUSTIN MARTYR (kwanakinsa a duniya wajen 100-165) ya shaida cewa Kirista da yawa a kwanakinsa sukan fitar da aljannu cikin sunan Yesu. Suka kori aljannun da suka fi karfin matsafa. Ku ji da kyau fa! KIRISTA KE DA IKON AIKATA WANNAN FIYE DA MATSAFA! YAUSHE ZANCEN NAN YA JUYE? ME YA SA? A wani littafi kuma Mallam Justin ya shaida cewa Kirista mata da maza suna da baye-bayne Ruhu har ma na annabci.**

**Wani bishop na Lyons a kasar Faransa mai suna Irenaeus (140-203) ya wallafa wani littafi, AGAINST HERESIES, wato GABA DA BIDI'A, cewa,**

> **Tabas ne da gaskiya wasu suke koron aljannu. Yawancin da suka warke suka zama membobin ikiliziya. Wasu suna iya duba abubuwa na gaba. Wato wahayi ya zo masu. Wasu suka yi annabci. Bugu da kari wadansu suka sa ma marasa**

lafiya hannu har suka warke. Har ma aka tada da wadansu matattu. Su kuwa suna nan tare da mu, mun san su. Bakinmu ya kasa yadda za a lissafta dukkan baye-bayen da ikiliziya ko'ina a duniya takan karba daga Ubangiji Allah.

Wani babban shugaba na da mai suna ORIGEN ADAMANTINUS wanda aka haife shi a birnin Alexandriya a kasar Masar a shekara ta 185 ya wallafa wasu littattafan da muke da su har wa yau. Ya bada shaida batun Kirista na zamaninsa cewa wasu suna fitar da aljannu, wasu kuma suna warkar da marasa lafiya da ikon Ruhun daidai da wanda ya zuga Isa Almasihu. Har yanzu kuma wasu ke duba ko annabci batun abubuwanda da za su auku nan gaba. A wani wuri kuma ya rubuta cewa a zamaninsa Mabiyan Kiristi suna da annabawa da kuma ma'aikatan mu'ujizai fiye da aka taba same su wajen Yahudawa.

Novatian (210-280) mai tauhidi ne wanda ya taimaki ikiliziya wajen koyarwar Trinity. Ya ce Allah na Trinity

> Shi ne wanda ya sa annabawa cikin ikiliziya, wanda ya koyar da malamai, wanda ya da baiwar harsuna. Ya ba da iko iri-iri har da warkaswa ga marasa lafiya, ya kuma aikata al'ajibai, yake gwada ruhohi, yakan raba ma gwamnati ikonta, yakan bada shawara da kuma yakan raba sauran baye-bayen Ruhu.

A mai da hankali yadda ya mai da wadannan duk baye-bayen Ruhu ne. Yawancin mutane masu maganar baye-baye a zamaninmu sukan bambanta tsakanin baye-bayen Ruhu da sauran iyawar mutum. Wai wadansu abubuwan da mutum ya iya ko ya koya ba na Ruhu ba, na halitta ne, na jiki ne. Mu Refom ba mu yarda haka ba. Dukansu na Ruhu ne domin Shi ne ya isad da mutum har ma mulki. Tushen wannan ra'ayi biyuntaka ne.

To, dai, shaidun Zamanin Ubanni sun yi yawa. Ga Tertullian (wajen 160-220) da Antony (251-356). Jerome ya rubuta tarihin wani mai suna Saint Hilarion (291-371). Ya shafa yau a idon matar da aka haife ta makaho, ta warke daidai yadda Yesu ya yi (Markus 8:23; Yah. 9:6). Jerome ya takaita magana da cewa, "Lokaci ya kasa mini in ba da labarin dukkan mu'ujizai da abubuwan al'ajibin da shi Hilarion ya aikata." Ambrose 339-397), Bishop na Milan a kasar Italiya, Turai, wanda a hannunsa ne Bishop Augustine ya tuba, yana goyon baya cewa a zamaninsa Allah ya raba ma mutane baye-baye kamar su warkaswa da harsuna. Ga kuma labarbarun da su Bishop Gregory na Tours (538-594), a kasar Farans, da Papa Roma Gregory I (540-604) suka bar mamu. Dukkan wadannan manyan shugabannin ikiliziya na Zamanin Ubanni sukan shaida mana cewa ikiliziyar zamaninsu ta kasance da ikon al'ajibai daidai da su Manzanni na SA.

Wani babban shugaban Ikiliziya ta Afirka ta Arewa, wato AUGUSTINE (354-430), Bishop a Hippo. Da farko ya rubuta cewa su ayyukan warkaswa da sauran mu'ujizai na SA aka dena yinsu. Ba a yi. Amma daga baya ya janye maganar cikin wani littafi mai suna RETRACTATIONS, wato JANYEWA, Ya ba da labarin mutanen da aka warkar da su daga ciwo dabam daban, na jiki da na ruhu duka.

Ya ce ba a rasa mu'ujizai a zamaninmu ba."

2. ZAMANIN TSAKIYA (MIDDLE AGES 600-1500)

**ST. FRANCIS OF ASSISI (1181-1226) sanannen mutum ne har wa yau saboda tsarkakken rayuwarsa. Shi kuwa ya kafa wata kungiya wadda tana nan har wa yau, wato Fransiskawa (Franciskan Order). Francis din nan ya aikata abubuwan al'ajibi da yawa. Ya warkad da shanyayyu yara da manya da dai sauran masu ciwo.**

**A zamanin kuma akwai wasu Kirista mai suna Waldensians. Kirista ne wadanda suna yaki gaba da mugunta cikin ikiliziya. Ba ruwansu da firistoci masu kawo rikice. An san su da halin biyayya ga Ubangiji. To, wadannan mutanen su ma suka yarda da wahayi da annabci da fitar da aljannu da kuma suka warkar da marasa lafiya ta wajen sa hannu da shafa mai.**

## 3. ZAMANIN GYARA (REFORMATION) NA WAJEN 1500 ZUWA 1900

**MARTIN LUTHER (1483-1546) ne wanda ya soma gyaran Ikiliziya. John Wimber ya nuna mamu yadda Luther shi ma yana bada gaskiya ga warkaswar ta wajen sa hannu da addu'a. Kuma bai ki annabci ba, sai dai kada a wuce gona da iri a yi musun bangaskiyarmu. Duk da haka dai, in ji Colin Brown, Luther bai nanata ikon mu'ujizai da warkaswa da yawa ba. A ganinsa lokacin mu'ujizai ya wuce, ba a yi kuma. Bai dauki zancen da muhimmanci kamar marigaya na Zamanin Ubanni da na Tsakiya ba. Na game da alkawarin Ubangiji ga almajirai a Yoh. 14:12, Luther ya rubuta cewa,**

> **Bana ganin wani abu mai muhimmancin cikin ayyukan almajirai wadanda suka fi na wadansu iko da daraja, musamman yanzu da shi ke zamanin al'ajibai ya wuce. Bugu da kari mu'ujizai ba su da ma'ana sosai da shi ke na jiki ne kurum kuma akan aikata su domin mutane kima.**

**Wato Luther ya yarda Isa Almasihu da almajiransa suka aikata al'ajibai, amma bai ga darajarsu ko amfaninsu sosai ba da shi ke sha'anin jiki ne kurum. Ga biyuntaka fa! Kuma lokacinsu ya wuce, ba a yi yanzu.**

**Mutane da yawa ba su goyi bayan Luther cikin al'amuran nan ba. Duk da haka dai a zamani biye da na gyaran ikiliziya kimiyya ya soma tashi. Yadda muka riga muka gani kimiyya ta zuga mutane da yawa su kyale duk abin da kimiyya ba ta iya gane ba. Rashin bangaskiya wajen Turawa ya soma tashi. Hankalin Kirista kuma ya soma rabu biyu.**

**IGNATIUS NA LOYALA (1491-1556) dan Ikiliziyar Roma ne wanda ya kafa Kungiyar Yesu (Society of Jesus). Ya ce,**

> **Ruhun Ubangiji yana zuga mamu inda ya ga dama, yana raba mamu baye-bayensu yadda yake so. Ba ya bukatar izini daga garemu. Saboda ya kamata mu farka muna a shirye kowane lokaci domin ya more mu cikin sabobbin ayyukan da yake tanajinsu. Mu ba za mu iya mu tilasa shi ya aikata abin da mu muke so ba. Asalin dukkan baye-bayenmu daya ne, wato Ubangiji da kansa. ABIN DA BULUS MANZO YA RUBUTA CIKIN 1 KOR. 12 YA SHAFE MU HAR WA YAU. Wannan surar ya kamata ta isad da mu mu rinjayi wasu mugayen halullukan da ke cikin zukatan shugabannin ikiliziya kamar kishin juna, rashin amince da juna, neman iko da kuma a hana mutum 'yancinsa ya yi aiki da baiwar da Ubangiji ya danka masa. Haka Ruhun ke nema a wajenmu. Kada mu hana ma Ubangiji abin**

da ya shirya. Yana iya bi da mu cikin hanyoyi dabam dabam. Shi ne jarorarmu cikin ayyuka, hafsoshi da baye-baye iri-iri. Ikiliziya ba soja ba ce. Wajen soja kowa ke sa riga iri daya, amma ba haka yake wajen ikiliziya ba, kowa ke sa nasa dabam. Wato Ruhu yaken isar da dukkan membobin ikiliziya ta wajen raba masu baye-baye dabam dabam. Ya kamata a ba kowa 'yanci su yi aiki da baiwar da Ruhu ya ba su. Wanda ya hana ya hana Ruhu ke nan.

Wimber ya ba da labarin wani VALENTINE GREATLAKES wanda ya mutu a 1638. Kirista ne shi a kasar Ingila. Yana da baiwar warkar da ciwon scrofula, wani ciwo ne na wuya. Daga baya kuma ya warkar da ciwuta iri-iri har mutane tuli suke zuwa wurinsa. Ko da yana aiki daga safiya zuwa yamma, lokaci ya kasa masa.

HUGUENOTS sunan zargi ne na Kirista na kasar Farans da suke goyon bayan Yohanna Kalvin. Yawancinsu talakawa ne, jahilai mara karatu. In sun yi magana nan da nan sai a gane da rashin iliminsu. Amma wadansunsu sai ka ce ciwon farfada ya kama su. An juma kuma sai sauki ya zo amma ba cikakke ba. Sa'anda suna cikin saukin din nan sai su fara magana cikin yaren Farans irin na masu ilimi ne, suka yi annabci ne na game da hukuncin da zai sami kasar Farans, suna fadin ayoyi daga cikin LMT wadanda irinsu jahilai ba su koya ba. Sai ka ce suna magana cikin harsuna kuma suna annabci, amma ba da saninsu ba ne. Sukan yi magana irin da jahilai da talakawa ba swu yi, babu tsoron kowa. Bayan da suka tashi ba su san abin da suka yi ko furta ba. Ko abokan gabansu ma suka ji su.

JOHN WESLEY ya kafa ikiliziyar Methodists. Ya fassarta dalilin da baye-bayen Ruhu suka ragu cikin ikiliziya. Ya ce dalili biyu ne. Da fari, bangaskiya ta yi sanyi. Na biyu, shugabannin ikiliziya suka ji kishin masu baye-bayen har suka yi masu zargi. Kuma da shi ke Ubangiji bai ba su nasu ba, suna musu gaba daya cewa ba yiwuwa, hauka ce kurum. Ba su amince da baiwar da Ubangiji ya ba memba amma bai ba shugaba ba. Ya ce ba wata aya cikin LMT wadda ta ce Allah ya dena raba baye-baye.

Amma a wannan zamanin kimiyya ta tashi. Kuma a kasashen Turai inda ikiliziya ta fi karfi a lokacin wani ra'ayi ya sami goyon baya wanda yake so a fassarta dukan halitta bisa ga dokokin da Ubangiji ya sa cikin halitta wadanda masu kimiyya kuma suna iya taunawa. Aka musu duk abin da ya fi karfin kimiyya. Wai ba yiwuwa ne kawai. Magana ta kare. Ko da yake mabiyan Kiristi ba su karbi ra'ayin nan duka ba, amma ra'ayin ya karye masu kafa. Bangaskiyarsu ta ragu. Ikonsu ya ragu. Da irin wannan bangaskiya suka zo Afirka da bishara mara iko da mara karfi. Bisharar da mu CRCN da sauran TEKAN muka gada ke nan.

## 4. ZAMANINMU NA YAU

Dr. CHARLES KRAFT mishanari ne na CBM na da wajen EYN. Har wa yau yana zuwa Nijeriya tare da Dr. Gilliland, tsohon Principal na TCNN, da wani kos domin pastoci da wasu manyan ikiliziya su sami digiri iri na Masters cikin fannin Mishan. Ko da yake ba memba na CRCN cikin kos din nan, akwai membobin TEKAN da yawa a ciki har da Janar Sakatarin TEKAN da kansa.

Shi Kraft din nan ya ga wata damuwa daidai da wadda ni da kaina na gani. Damuwar rashin ikon irin Kiristancin da mu mishanarai muka zo Nijeriya da shi. Bisharar da muka kawo sai magana, ba ikon warkaswa im ba jiyya ta kimiyya ba, ba ikon da

matsafa suke da shi.  Ana wa'azin ikon Yesu na warkaswa amma ba a taba gani ba sai a asibiti.  Ikon bishara sai ta wajen kimiyya, wato ta wajen hanya mai tsada, hanya mai injun iri-iri, amma ba taimako wajen maita, ba taimako ga wanda ke da tsoro a zuciyarsa. Shi Kraft bai yarda kimiyya ta sa mamu iyakar ikon da muke da shi. Ya ki bangaskiyar da mishanarai suka kawo cewa bangaskiyarsu ta kimiyya ce ba ta LMT ba ce.  Sukan bada gaskiya ga kimiyya fiye da LMT.  Abubuwan da aka nanata cikin LMT ba a kawo ba, aka kyale.

To, a wani gefe dai ina musun maganar Kraft domin shi bai ga dangantakar kimiyya da Ruhun Ubangiji ba.  Shi ya dauki kimiyya sai ka ce "secular" ne kurum, wato be dangantakarta da ceton da Ubangiji ya tanada mamu.  A nan ne ya kauce.  Amma inda ya nuna mamu yadda mu Turawan mishan muka kyale abin da LMT ya nanata na yarda da maganarsa.

Ban da kimiyya Kraft ya ga wadansu dalilan da suka hana mamu mu yi ayyukan al'ajibi, balle na warkaswa.  Ga halullukan da wasu warkaswar suka dauka da hanyar aikinsu.  Irin sujada na 'yan Karisismatikai sai ka ce ba sujada ba ne. Ga holo. Ga rawa, Ga abubuwa iri-irin da sukan aikata wadanda suka sa muna yi masu zargi.  Wani fasta ya ba ni labarin wasu saurayin Karisimatikan a garinsa wadanda sai ka ce suna farautar aljannu cikin majami'arsu har su matsa su a cikin kwanan dakin su kama su aljannun da holo da ihu don a kore su.  Kamar ana so a kama kare ko ana farauta dabban daji!  Muna jin tsoron irin wannan hali. Shi ne ya sa ba mu iya auna gaskiyar da akwai ba.

In kai fasta ka ce kana goyon bayan warkaswar ba wuya a yi maka kara cewa ka kauce daga hanyar da mishanarai na farko suka kawo.  Gaskiya ce ka kauce kuwa, amma lokaci ya yi mu duba da kyau ko kaucewar din nan daidai ne ko babu? Shugabannin ikiliziya kuma suka ce Martin Luther ma ya kauce!   I, ya kauce kam, ba shakka.  Ya kauce ne daga kuskuren ikiliziyar zamaninsa, amma bai kauce daga koyarwar LMT ba.

Har yanzu ga wani abin da ya hana mu aikin mu'ujizai. An koya mana cewa lokacinsa ya wuce.  Amma gaskiya ce kuwa?  Mun ga yadda yanzu wasu manya na Refom, har CRC da kanta, suna musun wannan ra'ayi yanzu.  CRC ta sake tunaninta ne bayan da ta kasa kunne a hankali ga tushen maganar Karisimatikai cikin membobinta. In ka ga rahoton da Majalisa CRC ta karba, sai ka ga yadda CRC ta ki abubuwa iri-iri nasu, amma a karshe ba ta iya yi musun ikon warkaswa da na harsuna ba.  Ba ta ga wani dalilin cikin LMT a ki su ba.  Sai ta yi nam'am da su, amma ban da wasu ayyuka da kuma ban da biyuntakar da suke aiki da ita.

Abu na uku wanda ya hana mu mu yi na'am da mu'ujizai, in ji Kraft, shi ne mukan nanata allahntakar Yesu, ba mu damu da mutumtakarsa ba.  Gaskiya ce kuwa.  In mun dauka cewa manyan ayyukan da shi Macecinmu ya yi ya yi su ne cikin matsayinsa na Dan Allah, to shi ke nan. Ba dama mu 'yan adam mu yi kwaikwaiyonsa. An juma kadan za a bayyana mamu ra'ayin Abraham Kuyper. Ya ce Yesu ya yi warkaswa da sauran manyan ayyukan cikin matsayinsa na dan adam. Ya zo ne don ya mayar mamu da iko na asali, ya tsarkake ikon, ya sabonta shi.  Duba yadda ya danka ikon ga almajiransa. Wato ba bakon iko ba ne.  Dan adam ya iya aikata su.  Ba wata aya ko daya cikin LMT wadda ta yi musun ikon nan.

Dalili na hudu shi ne rashin bangaskiya.  Ba mu amince da namu iko ba.  Mai yiwuwa ne wasu mutane ke da ikon warkaswar, amma sai masu bangaskiya wadda ta fi karfin

tamu bangaskiya. Tamu bangaskiya ba ta isa ba. Ba zan iya ba. Zan sha kunya. Za a yi mini zargi da ba'a. Kraft ya ce shi ma da ya ji tsoro haka. Amma ya shaida abin da ya faru da shi. Wata rana ya gaya ma Ubangiji cewa, "Ko na sha kunya a gaban mutane ma, ba zai dame ni ba. Sai dai kawai in yi maka biyayya kurum." MAIMAKON MU DAMU DA KUNYA, SAI MU DAMU DA RASHIN BANGASKIYA DA RASHIN BIYAYYAR DA MUKE YI MA UBANGIJI! Lalle ne kuwa, 'yan'uwa. INA AMSARMU?

A lokacin Kraft ya je kallon wasan kwallo. Wata yarinya cikin masu wasan ta gamu da wani hatsari har za a kai ta asibiti. Kafin aka kai ta, ta kira Kraft cewa ya yi mata addu'ar warkaswa, abin da bai taba yi ba. Ya ji tsoro amma ba dama ya ki. Sai ya yi mata addu'a. Tana jin zafin ciwon kwarai da gaske. An damu. Wai wuyarta ta karye. An dauka mata foto. Ashe, ba komai. Kuma ciwonta ya kare kawai. Kowa yana mamaki. Tun lokacin Kraft ya cigaba da warkaswa. Wadansu sun warke; wadansu ba su warke ba. Ba kunya kuma in wasu ba su warke ba. Shi dai yana cingaba da aikin da biyayya ga Ubangiji.

VICTOR H. ERNEST wani fasta ne na ikiliziyar Baftist. Shi ya wallafa wani littafi mai suna I TALKED WITH SPIRITS (Na Yi Magana da Aljannu). Ya sami goyon baya mai kyau don littafin nan daga wasu sanannun shugabanni. Saboda haka za a iya amince da littafin. Ernest yana bada labari ne yadda shi da kansa ya sadu da ruhohi da ikoki wadanda yawancin Turawa suke musun kasancewarsu. Ya ji maganarsu kuma ya ga ayyukansu da ikonsu. Manufarsa dai ya yi ma mutane gargadi cewa kada su kusance su domin ba wuya su sami iko a kan mutane masu kusa da su. Dalilin da ni na kawo maganar Ernest a nan don a tabbata cewa wadannan abubuwa suna nan ba shakka, komai shakkar Bature ko ta masu kimiyya, amma ba domin in zuga maku ku kusance su ba. Sunan abin da muke magana da Turanci shi ne ko "SPIRITUALISM" ko "SPIRITISM." Da Hausa akan ce da su masu duba da masu maita da masu sihiri (I Sam. 28:3, 7-8). Ernest ya ce wanda ya yi musun kasancewar wadannan ruhohi da ikoki jahili ne kurum, bai san abin da akwai ba.

Ernest kuwa ya ga abubuwa iri-iri masu ban mamaki. Wani lokaci yana cikin taron masu sihirin nan suna nema su yi magana da wata matar da ta rasu. Cikin dakin ga wani kafo na karfe (trumpet) a tebur. Sa'anda mai duba ya shiga aikinsa, sai kafon ya tashi ya soma tafiya cikin sarari cikin daki. Yana zuwa wajen wasu mutane yana yi masu rada. Sa'anda ya zo wajen Ernest, sai Ernest ya yi kokari ya kama shi, amma kahon ya tashi da sauri daga wurinsa. An juma kadan kuma ya dawo kusa da Ernest din nan har ya soma yin masa lacca na tsautawa cewa ba haka ya kamata a yi ba. Sai kuma kahon ya rada masa cikin muryar mataccen, amma Ernest yana shakkar muryar. Ya ga wani iko mai ban mamaki da kahon mai tafiya da kuma mai magana, amma ya sadu da rudi kuma na game da muryar mataccen.

A wani taro ya ga haskoki masu launi dabam dabam suna yawo a sarari cikin dakin taruwa. Kowane launi yana da ma'anarsa. Wani abokin Ernest ya kuma ga mahaifiyarsa wadda ta riga ta mutu. Ya gan ta ne cikin sakakken kamanninta. Da ganinta sai ya tada murya ya kira ta "Mama!" Da ya yi kokari ya rungume ta, sai ta bata.

A nan Afirika an san yadda da dare mutum yana kwanciya a gadonsa amma ruhunsa ko kuwa kurwarsa ta yi tafiya, jikinsa yana nan a gado bai tafi ko'ina ba. To, shi Ernest ma ya taba yi haka har ya shiga wani kasancewa dabam iri na ruhu. Ya ga wasu abubuwa mafi kyau wadanda bakinsa ya kasa fadi (kamar Almasihu Isa da almajiransa

a Mat. 17:1-3 da kuma Bulus Manzo a 2 Kor. 12:2-6?). Ya san mutum 2 wadanda kowane lokaci suna karatun wata jarida wadda ba ta fita ko ba, suna nisa da wurin da ake bugawar jaridar. A kasar Korea Ernest ya gani da ido yadda wani dan kasa wanda zai kori aljannu. Yana cikin kokarin sai wasu guntaye sanduna wadanda ke kwanciye a kasa suka tashi tsaye sa'anda shi mutumin ya kira sunan aljan din nan. Da Ernest ya tambaye shi inda ya koyi wannan aikin, sai mutumin ya nuna masa wadansu tsofoffin littattafai na da da.

Bayan da Malam Ernest ya tuba akan gayyace shi don wa'azi batun wadannan abubuwan da ya gani. Da farko kowane lokacin da zai yi wa'azi irin wannan akan dama hankalinsa da tunaninsa har

bai iya magana ba. Sai ka ce su alajannun da da yake koronsu ke so su hana masa wa'azi. Amma yakan kore su ne da addu'a cikin sunan Yesu. Da jin irin wannan addu'ar, sai suka tashi. Da wannan ya same shi haka, sai mata biyu sun furta laifinsu cewa da jin ayyar da zai yi wa'azi a kai suka firgita sai suka yi masa maita don su hana masa wa'azin. Da sun koma gida ikon shaidan ne ya fi karfinsu har daya ta yi kokari ta kashe kanta; wancan kuwa kanta ya juye. Sai bayan da suka furta laifinsu sun koma cikin hankalinsu.

Ernest ya ga abubuwa iri-iri masu ban mamaki, amma ya ga yawancinsu aikin shaidan ne, ba na alheri ba ne. Kuma ya ce rudi ya yi yawa da yaudara da zamba. Duk da haka dai akan aikata su wadannan abubuwa ba shakka. Ba yiwuwa a yi musunsu.

Ni mai shirin kos din nan na dauka wadannan ayyuka da ikon yinsu suna cikin ikon da Allah ya ba dan adam a loton halitta, amma saboda zunubi ne sun lalace. Yanzu yawancin masu aikata suna yi ba domin su bauta ma Ubangiji ko su inganta zaman dan adam ba. Amma bai kamata mu Kirista mu yi musunsu ba. Zai zama rudin kanmu muke yi. Mu duba yadda za a gyara su da ikon RMT, ya tsarkake su, mu mori wadannan ikoki cikin sunan Yesu Kiristi don ingantar da halittar Allah da zaman dan adam. Kuma kada a mance. Ikon kimiyya ya rage bukatar wadansu ayyukan irin wadannan. Inda kimiyya ya iya ya biya mamu bukata kada a kyale cewa muna son mu'ujiza ne. Ikon aikata mu'ujiza yana nan, amma ba za a nema don a ga darajarmu kawai ba (Mat. 12:38-39), sai da dalili, wato fitar da mutum daga cikin wani hatsari ko matsi.

### C. SHAIDAR MARASA BI A KASASHE DABAM DABAM

Ban da labarun da ke cikin LMT da kuma shaidu na tarihin ikiliziya daga farko har zamaninmu na yau, ga kuma shaidar marasa bin Ubangiji amma wadanda ko sun ma'aikata wadannan ayyuka ko sun tattauna ayyukan har sun tabbatar da su. Akwai wani mutum mai suna DOUCHAN GERSI. Bature ne amma ya yi girma a kasar Zaire a Afirka. Ya ga abubuwa iri-iri masu ba masa mamaki a can kasar Zaire har ya zartas cewa abubuwanda ya gani yana so ya tattauna su a wurare dabam dabam a duniya. Aikinsa ke nan ya tafi wata kasa ya zo kusa da 'yan kasa ya tone asiransu. Ya ga abubuwa iri-iri wadanda za a iya a mai da su mu'ujizai. Ya ga yadda aka kashe mutum da sihiri, wato bisa ga hanyar wadda da kyar Bature zai gaskanta, amma ya gani da ido--dole ne ya gaskanta. A idonsa wani mai warkaswa a kasar Filippines ya sa hannu cikin jikin wata marasa lafiya ba tare da ya yanka jikin ba. Kuma a idonsa ne mutumin ya fitar da kayan cikinta, ya duba kayan, ya yanka sashin da ba lafiya. Sai ya mayar da

kayan da hannunsa ba tare da aka yanka mata ba.  Bayan da ya gama ba wani tabo a jikinta kuma. Matar ta tashe ba ciwo ba komai.  Gersi ya ga wannan fiye da sau daya a kasar Filippino. Da Turanci ake ce da irin wannan "psychic healing."  A wajen Bature wannan ba zai yiwu ba, amma ya gani da idonsa.

Gersi ya ga mutum wanda ya fita daga cikin daki ta wajen bango daidai yadda Yesu ya shiga wurin taron almajiransa a Yah. 20:19. A cikin dan lokaci mutumin ya tafi wani gari mai nisa ya dawo da wani abin da shi Gersi da kansa ya ajiye kan tebur cikin wani daki cikin garin mai nisa din nan.  Da kyar Bature zai gaskanta irin wannan labari, amma Gersi ya gani da ido.  Dole ne.  Da idonsa ne ya ga mutane suna tafiya a sararin sama. Ba zai yiwu in takaita maku dukan abubuwan da ya gani ba.

Wata rana Gersi ya ga wani abin da ya ba shi mamaki, ba sau daya ko sau biyu ba. Sai ya tambayi mutumin da ya aikata abin. Mutumin ya amsa masa cewa, "Wata rana za ka gane da ainihin ikon ruhohi."  Hakika kuwa. Bature da kyar zai gane da su domin ya riga ya sayar da ransa ga kimiyya irin nashi.

RICHARD S. BROUGHTON wani furofessa ne wanda ya tattauna abubuwan da masu kimiyya sukan kyale, ba su taba ba, wato sha'anin sihiri da sauran ikoki iri-iri.  Shi dai yana kokari ya tone su bisa ga hanyar kimiyya mai suna PARAPSYCHOLOGY.  Ba wai don ya bada gaskiya ga LMT ba, amma don ya gan su da ido ne, bai iya musunsu ba. Masu kimiyya kuwa ba su amince da irin wannan kimiyyar din nan ba.  Shi ne ya sa ya kira wannan kimiyyar "controversial," wato ana gardama akai, ba a karba sosai ba. Amma shi Broughton bai iya bari ba domin ya gani da ido.  Ya ce 'yan adam suna fama da abubuwa masu ban mamaki tun farkon zamansu a duniya, suna ji, suna gani, suna aikatawa.  Yaya za a yi musun abubuwan da mutane ko'ina suka gani?

Mene su abubuwa na ban mamaki wadanda Broughton da wadansu mutane suke tone?  Ba dama in kawo su duka a nan, sai wasu misalai ne kurum.  Ga misalin mafarki. Wata mace ta yi mafarkin jikarta sai ka ce ya na bakin mutuwa cikin gadonsa a gidan iyayensa. Gidan kuwa ya yi nisa da matar.  Ta farka ta yi tunanin jikar, amma ta dauke kamar mafarki ne kurum, ba abin da ya faru.  Amma zuciyarta ba ta kwanta ba. Sai ta buga ma danta, baban yaron, waya a tsakar dare domin ta kwantar da hankalinta. Danta ya gaya mata yadda abin ya faru daidai mafarkinta!

Broughton yana da labarun mafarkai irin wannan da yawa.  Wani ya yi mafarkin jirgin tudun da ya fadi cikin kogi. Washegari ya ji labarin hatsarin jirgin. Wurin hatsarin, lambar jirgin, yadda mai tuki ya kubuta da rai da dai sauran abubuwa daidai da mafarkin.  KO KA TABA YI MAFARKI HAKA? KO KAN SAN MUTUM WANDA YA YI?

Amma sanin abubuwan da ke faruwa a wani wuri ba sai da mafarki ba ne. Ga wata macce wadda ta rabu da mijinta da dadewa. Ba ruwansu da juna, ba labarin juna.  Wata rana ta na tare da danta. Ta yi ihu sai ka ce wani mugun abu ne ya faru.  Danta ya tambaye ta, "Mama, me ya faru?"  Ta amsa cewa, "Ai, babanka ya yi aure yau."  Danta bai gaskanta ba. Sai ya bincika zancen. Ashe, gaskiyarta, ya yi aure a wani wuri mai nisa.  Ta yaya ne matar ta san wannan? Ita ba mai duba ba ce.  Ita da kanta ba ta san yadda ta ga abin ba.

Wata rana wata tica a makaranta ta ji wani zafin ciwo a kafadarta da kirjinta ba labari. Zafin ciwon ya sa ta yi ihu har abokan aikinta sun gudu zuwa wurinta su san abin da ya faru.  An juma kada sai ciwon ya warke.  Ashe daidai lokacin wani kawonta wanda yake

a wani wuri mai nisa ya gamu da ciwon zuciya ya mutu. KO KA TABA JIN LABARIN IRIN WANNAN? Na tabbata irin wannan yana faruwa a nan Nijeriya. INA ASIRIN ABIN? Wadannan sun faru ne a kasar Amirika inda yawancin mutane suna musun irin wadannan abubuwa. Wadannan misali kadan ne kurum daga cikin labarun da Broughton ya bayar na abubuwa masu ban mamaki wajen Turawa. In ji yawancin Turawa, rudi ne kurum, karya ce. Ko kuwa za su ce mai labarin ya haukace. Amma Broughton ya kawo misalan da aka riga aka bincika su, sun tabbata, ba shakka. Shi kuma yana ba da labarin masu warkaswa irin na Filippines wadanda muka riga muka ji daga Gersi. Ya sani akwai masu rudi, amma binciken da aka yi ya tabbatar mamu cewa komai yawan masu rudi, akwai masu gaskiya a ciki a Asia da Amirika ta Kudu.

Labarun Broughton dai ba za su kare ba. Wani mutum jakarsa ta bata masa, amma wani wanda bai yi kusa da jakar ba ya iya gani inda yake. Ga labarin tebur mai tafiya a sarari (levitation) da sauran abubuwan da shi Fasta Ernest ya ba mu labarinsu.

Ikiliziyar Roma takan kebe wasu mutane takan kira su tsarkakakku (saints). Mutane ne wadanda suka aikata ayyukan bangaskiya fiye da sauran mutane har ayyukansu suka nuna suke da tsarki musamma. Da yawa cikin su tsarkakakku sukan aikata mu'ujizai iri-iri. Wasu suke tafiya cikin sarari. Ga labarin Tsarkakakku Yusuf na Copertino wanda yakan hau sarari cikin taron sujada a idon jama'a duka. Manya ba su ji dadin abin ba suka sa shi cikin foro. Urban VIII, wani Papa Roma, shi ma ya gani tare da wadansu marasa bi. Jakadan kasar Spain wajen Vatikan, wato gidan Papa Roma ke nan da shi da matarsa suka gani har matar ta suma. Wani sarki a kasar Jamus, memba ne na ikiliziyar Luther, ya ji labarin Yusuf. Ya je wurin ya boye don kada a ganshi. Da ya gani, sai ya rabu da ikiliziyar Luther ya zama memba na Roma.

A tuna fa: shi Broughton ba Kirista ba ne. Amma yana karban rahotannin Ikiliziyar Roma na game da wannan batun domin ya ga yadda suka tattauna raywuwar mutum da ayyukanta kafin su kebe ta. Kamar kotu ne inda akwai wani mutum mai matsayin Promotor Fidei, wato "Mai Ingantar da Bangaskiya," wanda aikinsa ne ya karyatar da dukan labarun da aka kawo akan mutum don a kebe shi, sai ka ce bai aikata ba daidai da su lawyoyi sukan yi a kotu. Kusan Ikiliziyar Roma ba ta cika so a kebe mutum tsarkakakke ba, sai in ya zama mata dole ne. Ta sani wadanda suka kawo sunan mutum don a kebe ta ba wuya su kawo labarinsa iri-iri wanda ba gaskiya. Sai wanda ya gagara ki, shi ne za a kebe.

Daya daga su Masu Ingantar da Bangaskiya mai suna PROSPERO LAMBERTINI ya wallafa wani littafi inda ya bada labarin ayyuka masu ban mamaki da aka yi. Dukan abubuwan da muke ji a nan Nijeriya suna ciki. Kuma ya ce, "Sanin abubuwa na gaba da na jiya da wadanda suke da nisa da kuma wadanda ke boye cikin birnin zuciyar dan adam" ba sai tsakarkakku ba. Binciken da ya yi ya nuna mutane iri-iri suna da irin wadannan baye-bayen, komai bangaskiyarsu ko addininsu.

Sha'anin maita ba na Afirika kadai ba. Turawa ma suna da shi. Sai dai yawancin Turawa na zamanin yanzu ba su san tarihin din nan wajensu ba. Wani mai suna HUBERT J. DAVIS ya wallafa wani littafi mai suna AMERICAN WITCH STORIES inda ya rubuta labarun maita iri-iri na wasu talakawa a kasar Amirika a jihar Virginia da na wadansu wurare. Kuma ya ce binciken da aka yi ya nuna cewa wadannan abubuwa Turawan Amirika suka zo da su daga can kasashen Turai (Europe) inda da suka fita. Dukan ayyukan da masu maita sukan aikata a nan Nijeriya a can ma sukan yi. Sai dai a can sha'anin ya hadu da addinin Kiristanci. Kowane lokaci akan kori aljannu da addu'a

ga Ubangiji cikin sunan Triniti. Maita suna nan, amma sau da yawa akan rinjaye su da bangaskiya da addu'a. Amma wani lokaci kuma akan kore su ne da magani dabam dabam.

TOM BROWN wani Ba-amirika ne wanda tun yarantakarsa ya shiga hannun wani shehun malami na 'yan kasar Amirika na asali wadanda ake ce da su "Indians." Su Indians din nan suna da addininsu na gargajiyya iri na tsafi kusa da namu a nan Nijeriya. Tom Brown ya ce da shehun "Grandfather," wato "Kaka." Shi Kakan ya koya ma Brown sha'anin asiri iri-iri, amma na nagarta ne, ba na mugunta ba. Saboda abubuwan da ya ji ya gani Brown ya rabu da ra'ayin Turawa. Ya ce akwai abubuwan da mutum ba zai iya taba da hannu ba, ba zai iya gani da ido ba, abubuwa na ruhu wanda mutum wanda ya ki komai sai kimiyya ba zai iya gane da shi ba. Amma kafin Kaka ya koya masa sha'anin ruhu, ya koya masa asirin rayuwa a daji har sai ka ce daji ya shiga zuciyarsa ya gane da abubuwa na daji iri-iri. Ya koya hankuri irin da ake bukata a daji, kamar jin yungwa, ganewa da dabbobi da itatuwa da ciyayi. Ya san wadanda za a ci su da kuma wadanda suna da magani da sauran amfaninsu. Har ma yakan hau itace masu tsayi sosai. Sa'anan zai yi tsalle daga itace zuwa itace kamar biri.

Kakan kuma yana da baiwar warkaswa. Wani ya yanka masa kafa da zurfi har jini ya zubar kamar zai mutu. Sai Kakan ya mike kafarsa. Da hannu daya ya rufe raunin; da wancan hannu ya share jini. Sai jinin ya tsaya. Ya daura raunin da wata fata. Ya tashi yana tafiya sai ka ce ba abin da ya faru. Washegari ya kwance fatar. Ga tabo, amma kafin wata ya kare tabon ma ya warke. Brown ya tambaye shi asirin warkaswar nan. Kaka ya amsa cewa, "Sha'anin bangaskiya ne kurum." Bangaskiya ta fi jiki karfi. In kana da bangaskiya, bangaskiyar zai yi ikon jikinka. In ka dauka cewa ga wani abin da ba za ka iya ba, to, dai, haka ya kasance. Ba za ka iya ba ke nan. Amma abin da ka gaskanta ka iya, to, za ka iya mana. Asirin duka shi ne bangaskiya. Har yana tafiya cikin wuta, amma jiki bai yi rauni ba.

A takaice dai shi Kakan ya iya abubuwa iri-iri. Ya ga abubuwan da suka yi nisa da shi. Ta yaya ne ya san su? Ya koya ne ta wajen mai da hankali ga halittar Allah shekara da shekaru har wata dangantaka ta dayantaka ta kafu tsakaninsa da halitta-- daji, itatuwa, dabbobi, duwatsu da dai sauran abubuwa na daji. Wato abubuwan da ya iya da abubuwan da ya san su ba bakin abubuwa ba ne cikin halitta.

A nan Nijeriya 'yan kasa sukan aikata abubuwa masu ban mamaki da yawa. Akwai asiri dabam dabam da ikoki wadanda masu kimiyya ba su gane ba kuma suna musunsu. Akwai na alheri, akwai kuma na duhu. Ku 'yan kos din nan kun fi ni saninsu. Ba bukata ni in bayyana maku. Gara ku ku fassarta mini su, amma da kyar za ku fada a kunnena domin kun sani cewa Turawan Mishan ba swa so su ji wannan magana. In sun ji ma, sai da fada. Amma a yau sha'anin ya sake. Turawan yau ba iri na da ba ne. Mishan na yau dabam da na jiya. Mun fara ganewar da kuskurenmu.

Mun yi dan zagaya cikin duniya. Mun duba yadda ikiliziya takan dauki al'amuran mu'ujizai daga farkon tarihinta har zuwa yau. Yanzu lokaci ya yi mu dawo gida, mu duba yadda mu Refom muke daukan wadannan al'amuran.

D. SHAIDAR REFOM (Reformed)

In za mu tattauna ra'ayin Refom game da wannan zancen, ya dace a fara da YOHANNA KALVIN, baba na Ikiliziyar Refom. Kalvin bai yi musun al'ajibai na cikin LMT ba. Kuma ya sani mutane iri-iri suna da ikon aikata al'ajibai, ba Kiristi da mabiyansa kadai ba. Amfanin mu'ujiza shi ne a daukaka Ubangiji. Wadanda ba su girmama Shi ba na shaidan ne, ba ruwan Kirista. Amma yanzu ba al'ajibai, ba bukatarsu da shi ke Bishara da ikiliziya sun kafu.

Kalvin ya nanata cewa Kiristi ya aikata mu'ujizai da ikon allahntakarsa, but na mutumtakarsa ba. Ikon da annabawa da manzanni suka yi amfani da shi ya fito ne daga Allah da kansa wanda ya isar da su, amma ba ikon mutumtakarsu ba ne. Tushen ikon ba na halitta ba, na ruhaniya ne.

A bayan Kalvin su masu goyon bayan tauhidi nasa akan ce da su da Turanci "Calvinists." Sun yi karfi a wadansu kasashen Turai, musamman a kasar Switzerland, Netherlands da Ingila, balle a arewarta, wato Skotland. Na kasar Ingila ake ce da su "Presbyterian"; na kasar Netherlands da Switzerland "Reformed" ko kuwa "Refom." Daga baya wadansu suka kaura zuwa wasu kasashe, suka kafa ikiliziyarsu. Refom na Netherlands suka tafi Amirika da Kanada da kuma Afirka ta Kudu. Presbyterians su ma suka tafi Amirika da Kanada. Saboda haka a can Amirika da Kanada za ka same su Refom da Presbyterian duka. Asalin Christian Reformed Church a kasar Netherlands ne, amma suka tashi zuwa Amiriki da Kanada.

Daga can kuma suka aiko mamu mishanarai a nan kasar Nijeriya. Suna aiki da Christian Reformed Church of Nigeria har wa yau. Shi ne ya sa mishanaran da ke aiki da CRCN suka zo daga kasashen Amirika da Kanada da Netherlands. Refom na Afirika ta Kudu su ma suka zo Nijeriya, suka kafa NKST. Amma saboda rikicensu na wariya suka koma gida suka danka ma SUM-CRC aikinsu.

Presbyterians na Skotland, wato kasar Ingila ta arewa, suka aiko da mishanarai zuwa kasar Nijeriya wajen Calabar, suka kafa Presbyterian Church of Nigeria wadda muke santa yanzu. Suna tare da mu a TCNN.

Sunan "Presbyterian" ya nanata irin mulkin da Kalvinists suka kafa, wato na "presbyter" ko kuwa na dattibai na kowane gu. Wato sunan ya nuna cewa ba su yarda iko cikin ikiliziya ya taru wajen mutum daya ba, kamar ko Papa Roma ko Bishop, amma ikon ikiliziya yana hannun dattibai tare, ba hannun mutum daya ba.

Sunan "Refom" kuwa ya nanata cewa gyarariyyar ikiliziya ce kuma kullum take gyaran kanta. Ba lokacin da bata bukatar gyara. Kirarin Refom da wani tsohon yaren Latin (Romanci) shi ne "Semper reformanda," wato "kullum sai gyara," ko kuwa "always reforming." Saboda haka bai dace ba ne ikiliziyar Refom ta tsaya kan hanyar da ta soma da ita tun farko. Refom wanda ta san tushenta ba za ta dauki halin da ake ce da shi "conservative" ba. Idan damuwa ta tashi kada a kyale kawai cewa ba haka aka koya mamu ba. A duba damuwar sosai a san yadda za a gyara, amma kafin a yi gyarar, sai a tattauna abubuwa guda biyu. Na farko, me LMT ta ce? Na biyu, ina dalilin da aka kafa matakin da ta kawo damuwa yanzu? Da ta yi maganin me?

To, muna tattauna zancen mu'ujizai da na al'ajibai. Mun riga muka ga yadda aka yi cikin ikiliziya ta da da kuma ta zamaninmu na yau. Yanzu muna son mu duka musamman ra'ayin Refom. Amma idan za a bi darikan Refom duka, lokaci zai kasa mana. Saboda haka ban sa maganar Presbyterian a ciki ba, sai maganar Refom wadanda mu a Nijeriya muka san su, wato Christian Reformed Church da iyayenta, wato Refom na kasar Netherlands inda aka haife ni mai tanadin kos din nan. Da

yarenmu sunan darikar shi ne Gereformeerde Kerk, wato Reformed Church. Ita ce ikiliziyar da ta yi mini baftisma. A yau haka mu CRCN da NKST muna da damuwa na game da batun abubuwan da su Karisimatikai suka kawo mamu. Sai ka ce saurayenmu sun fi son Karismatikai da Refom. Da yawa sun fita daga cikin CRCN suka shiga darikan Karisimatikai. Ba su gane da tushen Reform ba; ba su kuma san tushen Karisimatikai ba. Ai, to, dole zai zama haka. Ba halin saurayi ba ne ya kimtsa hankalinsa wuri daya ya tattauna ya yi addu'a har Ubangiji zai nuna masa haske. Wajen sauraye komai sai da sauri. Halittarsu ke nan. Kada a ga laifin halin wannan. Kai da kanka da ma kana da wannan halin.

Alhakinmu mu manya ba shi ne a hanna saurayenmu kawai ba, a aza masu dokoki iri-iri. A saurare su a hankali don a gane da abin da ya dame su cikin Refom da kuma maganin da suke samuwa wajen Karisimatikai. Sa'anan kuma a san irin maganin da za a kawo, maganin da zai dace da tushen rukunan Refom. Za a duba ko muna bukatar mu sake tunaninmu a wani gefe? Ko muna bukatar gyaran hanyar aikin da ake yi? Amma ba zai yiwu ba kawai a ce haka kakani suka kafa mana, haka za mu cigaba har abada, ba sakewa, ba gyara. Halin nan zai kashe mu.

Da dai yawancin manyan masu tauhidi na Refom ke goyon bayan Luther da Kalvin cewa lokacin mu'ujizai ya wuce, ba a bukata yanzu. Amma tun da Karisimatikai suka tashi suna zuga darikai su sake tattauna batun har Refom ma sun gani ya kamata a yi haka. Saboda haka a zamaninmu na yau Kirista ke magana da yawa batun baye-bayen RMT. Da dai su baye-bayen suna nan, Ubangiji ke raba mamu, amma hankalin ikiliziya baya a wurin yadda yake yanzu. Amma yau dole ne mu mai da hankali garesu da kuma mu gane da su. Balle shugabannin ikiliziya. Tun wajen 1960 Karisimatikai sukan tilasa sauran Kirisita su san abin da LMT ke ce da baye-bayen RMT. Fastan da ya kyale zancen nan ko kuwa shi jahili ne na game da su baye-bayen zai sha wahala cikin ikiliziyarsa har ma membobinsa za su tashi su bar shi su shiga daya daga cikin darikan Karisimatikan da suka tashi a wannan zamanin.

Su Refom na kasar Netherlands, wato Gereformeerd, a wajen 1900 suna da manya shehunan tauhidi, wato Furofessa Abraham Kuyper wanda an riga aka ji labarinsa da kuma Furofessa HERMAN BAVINCK. Dukansu biyu suka mutu wajen 1920, amma har wa yau masu tauhidi na CRC a Amerika da Kanada wadanda ba su manta da yaren Dutch ba suke sauraronsu. Kamar ni bana rubutun komai sai dai in bincika nasu littattafai ko. Su ne manya nawa wajen tauhidi, fiye da shi babanmu Kalvin. Haka ma da CRC da kanta. In za ta tattauna wani abu dole ne ta karanta nasu littattafai. Na riga na bayyana dalilin da mu a CRCN ba mu da labarin Kuyper. To haka ma da Bavinck. Amma ba dole ba ne in yi na'am da dukan ra'ayinsa. Akwai wurin da ba zan karbi maganarsa ba. Kowane mutum dai sai ya auna abin da yake karatu.

Ga takaitattun abubuwan da shi Bavinck ya fada game mu'ujizai. Ya ce dukkan ayyukan Allah mu'ujizai ne har ma ayyukansa cikin halitta (Zab. 77:13-14; 107:24; 139:14). Wato ba wai abubuwan da sun fi karfin kimiyya su kadai ba, amma dukan ayyukan da Ubangiji yake yi LMT ya ce masu banmamaki ne. Ayyukan Ubangiji cikin halitta da mu'ujizansa ba kishiyoyi ba ne. Ko in kimiyya ta iya gane da wani abu cikin halitta, har yanzu mu'ujizar Ubangiji ne. Duk da haka dai ayyukan Ubangiji na kullum da ayyukansa na loto-loto wadanda sukan nuna ikonsa musamma bisa ga hanyar da ba a saba ba (extraordinary show of power) dabam ne.

Allah baya wasa da halittarsa.  Ya aza mata dokokin da halitta ke bi kowane lokaci. Rana takan bullo kowace rana, tana tafiya a sarari daga gabas zuwa yamma, sai ta fadi kuma.  Kowace rana, ba fasawa.  Dukan halitta ke biyayya ga dokokinsa ba fasawa (Far 1:26-28; 8:22; Zab 104:5, 8-9; 119:89-91; 148:1-9; M. Had. 1:9-10; Ayub. 38:8-11 da dai sauransu).  Amma ban da wadannan

ayyukansa na kullum, ga abubuwan da yakan aikata masu ban mamaki na lokaci-lokacin. Duba Fit. 34:10. Mene ne al'ajibin da Ubangiji zai aikata?  Zai kora ma 'yan Isra'ila dukan abokan gabansu.  Duba kuma bambancin mutuwar da ke gaba kowa da mutuwa inda duniya ta bude bakinta ta hadiye masu zunubi a L. Kid. 16:28-30.

Bavinck ya cigaba da magana cewa in ji LMT ko mutanen da ba su san Allah ba su ma ke da ikon aikata al'ajibai. A tuna da ayyukan masu maita a fadar Fir'auna. Duba kuma Mat. 24:24 da W. Yoh. 13:13ff.  Duk da haka dai Ubangiji shi kadai ke aikata su, amma yan isarda mutum (Zab. 72:18; 77:12-13; 136:4).

Tushen al'ajibai da farawarsu halitta ne kuma yadda Ubangiji ya kiyaye dukkan halittar. Halitta da kiyayewarsa da kansa al'ajibai ne. Ba wai al'ajibi bakon abu ba ne a halitta.  Wadansu suna cewa al'ajibi aikin ruhu ne, ba ruwan halitta. Amma Refom ba mu yarda da haka ba.  Su al'ajiban sukan faru sai ka ce dami-dami ne.  Ko da yake suna faruwa kowane lokaci, amma a wadansu zamanai sukan auku da yawa kamar a zamanin Annabi Musa, Annabi Iliya da Annabi Elisha. Sa'anan kuma ga su da yawa a zamanin Ubangiji da manzanninsa.  Su mu'ujizan annabawa na TA alamu ne na nasarar Ubangiji kan shaidan.  Sun auku sai suka wuce. Ba abin da ya sake cikin tushen zaman duniya da dan adam.  Amma da zuwan Yesu ga cikakken dan adam na gaskiya, gyararre, Cikinsa duniya da dukkan halitta suka gyaru, aka sasanta su da Mahaliccinsu.  Cikinsa halitta ta sake tashe daga zurfin faduwar da ta yi ta koma cikin darajarta irin ta asali.  Cikin Yesu wani ikon Allah ya bayyanu wanda ta fi dukkan halaka da barnar mugunta karfi.  Yesu ya ci nasara kan wannan muguntar ba a wani gefenta ba, amma a tushenta ne. Bayan da ya hau sama duniya ba ta cigaba kawai ba kamar ta yi  bayyan al'ajiban annabawa na TA.  A'a, manzanni suka cigaba da wannan ikon da kuma a bayan zamaninsa ana cigaba da ikon cikin ikiliziya. Amma da ikiliziya ta kafu sun soma raguwa har daga baya suka tsaya, shi ke nan, ba sauran bukata.

An riga aka gabatarda Dr. Abraham Kuyper.   Ko da yake shi Kuyper da Bavinck suka yi na'am da juna kwarai da gaske, a wannan fannin ba su yarda da juna ba.  Ra'ayin Kuyper din nan ya ce har wa yau ana iya aikata mu'ujizai.  Ya ce mu'ujiza abin mamaki ne kuma ba abin mamaki ba ne.  Abin mamaki ne domin yawancinmu ba mu gane da hanyar da ake yinsu ba kuma ba a cika ganinsu ba, sai loto-loto.

Amma tushensa ba abin mamaki ba ne.  Duba ikon Adamu wanda ke mulkin dabbobi har ya rada masu sunayensu.  Shi ne ikon da Ubangiji ya ba mu tun farko.  Sai dai saboda zunubi ne muka zama bayin halitta kamar yadda na riga bayyana a sama. WATO IKO NE NA DAN ADAM TUN FARKON HALITTARSA, BA BAKON IKO BA NE. Adamu yana aiki cikin matsayingsa na mutum mai mulkin halitta.  Bayan faduwar dan adam cikin zunubi wannan ikon ya bata wajen yawancin mutane, amma ba wajen duka ba.  Wasu sun rike ikon, amma maimakon su fito a fili su nuna ma mutane yadda sukan aikata, yawancinsu sukan mai da ikon sha'anin asiri ne wanda suke moronsa ba domin alheri da nagarta ba, amma domin mugunta da aikin duhu da na rudin jama'a.  Yadda zuriyar Lamek suna cigaba da himmantar da halitta (Far. 4:17-24) amma da fahariya ne ba domin su bauta ma Ubangiji da abubuwan da suka bullo da su ba, haka yawancin

masu ikon aikata al'ajibai suke yi.  Duba musamma masu sihirin Fir'auna da sauran da aka riga aka ambata su a sama.  Ban da na LMT ma ga abubuwan da ake aikatawa wajenmu a Afirika.  Amma wasu masu ikon kuma ke amfani da shi cikin gaskiya. Duk yawancin wadannan iko ne na asalin halitta, ba bakon iko ba ne.  Sai dai muguntar da ta faye zuciyar dan adam ta sa aka mai da ikon abin tsoro ne, abin asiri, abin zalunci, aikin duhu, ba na Allah kuma ba.

Shi ne ya sa Ubangiji ya hana mamu mu yi aiki da irin wannan ikon. Duba Littafin Firistoci 19:26-31; Maimaitawar Sh. 18:10-14.  Maimakon a zo wajen ma'aikatan wadannan, Ubangiji ya ce, "Zai tayar muku da wani annabi kamata (wato kamar Annabi Musa ke nan) daga cikin jama'arku, su ku saurare shi."  "Zan sa magana a bakinsa, zai fada musu duk abin da na umarce shi" (M. Sh. 18:15, 18).

To dai, Ubangiji ya cika masu wannan alkawarin ta wajen annabawa na cikin TA. Wadansunsu suka aikata manyan abubuwa na al'ajibi. Ya cika alkwarin nan musamman ne ta wajen Dansa Isa Almasihu, shi wanda ya aikata manyan mu'ujizai. Biye da shi kuma ga su almajiransa ko kuwa manzanninsa da sauran ikiliziya masu aikata al'ajibai.

Amma fa sai a lura da kyau.  Mu'ujizan Annabi Musa da na sauran annabawa na cikin TA ayyuka ne na dan adam wadanda suka aikata da ikon da Allah ya aza masu tun farkon halitta, amma ya bata saboda zunubi. Allah ya mayar masu da wannan ikon.  Iko ne na halittar dan adam, ba bakon iko ba ne.  HAKA MA DA NA ISA.  YA AIKATA SU NE CIKIN MATSAYINSA NA DAN ADAM, BA NA DAN ALLAH BA.  Ikon da shi ya ba Manzanni da sauran ikiliziya iko ne wanda tushenta shi ne halitta.

Saboda haka yanzu muna da ikon aikata abubuwa fiye da wadanda Yesu ya yi.  Mu wadanda RMT ya sabonta mu muna da ikon da aka bayar tun farkon halitta.  Kuma muna da ikon kimiyya wadda ita ma ta bullo ne daga 'yancin da RMT ya yi mamu a zukatanmu. Yanzu muna da waddannan iko guda biyu. Ta wajensu ne muna iya cika Umarnin Ingantar da Halitta.  Ta wajensu ne Ubangiji ya cika mamu alkawaransa.

Wadannan shehunan masu tauhidi, wato Furofessa Bavinck da Furofessa Kuyper suka wallafa littattafai masu yawa wadanda suna nan har wa yau.  Suna da tasiri mai yawa cikin CRC na Amerika ta Arewa.  Sai zancen mu'ujizai da na warkaswa da na harsuna ya tashi wajen 1960 zuwa gaba.  An dama darikar kwarai da gaske. Rigima da gardama suka rikitar da ikiliziyar ainun.  A wadansu gu ba a so a ji sabon maganar da ta tashi har masu harsuna da sauransu da yawa suka tashi zuwa darikan Karisimatikai. Wasu dangi suka rabu biyu kan zancen nan, ba ruwansu da juna.  Wadansu 'yan'uwana suna ciki kuma suna so su bar CRC.  Da na koma Kanada domin hutu na bi wasu fastoci na tsauta masu yadda a waje muna ginin ikiliziya, amma a gida suke rusar da ita har suna koron 'yan'uwana.  Ya kamata su yi tunani da zurfi irin da ya dace da Refom, su tattauna abin da kyau su nemi manufar Ubangiji su san yadda za su biya bukatar wadannan membobinsu su shirya masu fili.  Mu masu magana haka mun yi dan yawa har Majalisa Babba ta kafa wani kwamiti wanda za ta tattauna zancen nan da zurfi bisa ga tushen Refom.

A shekara ta 1973 Majalisar CRC ta yi na'am da rahoton da kwamitin suka shirya cewa,

> LMT  ya koya mamu cewa ko a zamaninmu ma Ubangiji ya iya aikata mu'ujizai da al'ajibai.  Har yanzu muna cikin zamanin SA. Har yanzu RMT ke mulkin ikiliziyarsa, yana iya karfafa bangaskiyarmu yadda ya ga dama.  Shi wanda ke aiki a zukatanmu yana iya aikata fiye da dukkan roke-rokenmu da kuma fiye da

muke sa tsammani (Af. 3:20-21). (Duba ACTS OF SYNOD, 1973, pp. 456-457. Sai kuma a duba ayar din nan.)

**Wato Majalisar ta bude kofa ke nan. Ya kamata mu CRCN mu bincika rahoto nasu mu san yadda mu za mu yi da wannan zancen. Daga baya halin CRC ya sake. Ba a jin tsoron wadannan abubuwa kamar da. Wadansu gu yawancin membobinsu na Karisimatikai ne. Hanyar sujadarsu ta sake. Suna buga tafi. Suna amfani da gita da ganga da sauran abubuwa na kida. Suna daga hannuwansu da yabo. Suna amsa mai wa'azi da "Amin." Sun sami 'yanci fiye da da. Bayan da CRC ta yi na'am da rahoton, yawancin membobin kuma suka dena gudu zuwa waje. Yanzu suna da fili cikin CRC. Ba a matsa su kamar da.**

**Ban da Majalisar CRC da kanta ma wasu manyan masu tauhidi na CRC suka wallafa wasu littattafai masu goyon bayan warkaswa da mu'ujizai cewa ba abin da ya hana. Marigayi Dr. GORDON SPYKMAN furofessa ne a Calvin College wanda ya rasu a watan Yuli, 1993. Shi mutum ne mai daraja wanda akan saurari koyarwarsa sosai. A shekara ta 1992 ya bullo da wani babban littafi mai sunan REFORMATIONAL THEOLOGY. Ga abin da**

**rubuta:**

> **LMT ba ta koya mamu cewa ikon Allah na aikata abubuwan al'ajibai sai zamanin da, wato na zamanin LMT ke nan, da kuma sai a wadansu wurare masu nisa, wato kasar Yahudawa, ba. In mun ce ba a aikata wadannan a yanzu, ai, muna goyon bayan wadanda ke da ruhu na kin Ubangiji (secularism). Ana iya aikata ayyukan al'ajibi da na warkaswa a yau daidai da zamanin da. Bai kamata mu bada nasara ga wadanda ke cewa ba gaskiya kuma ba iko wadanda kimiyya ba ta sansu ba (secularists). Im an ba wadannan nasara, ai, an rage karfin addu'a ke nan (p. 296).**

**Dr. ALBERT WOLTERS furofessa ne a Redeemer College, wata jami'a wadda membobin CRC suka kafa a kasar Kanada. Ga abin da ya bayyana mamu cewa yawancin mutane masu maganar baye-bayen Ruhu suke nufin ayyuka masu ban mamaki kamar su harsuna, annabci da warkaswa. Ra'ayi na game da wadannan ya rabu biyu. Ra'ayi daya ke cewa wadannan baye-bayen suka sauko daga sama ne (supernatural); ba su fito daga halitta ba. Kuma darajarsu ta fi na wasu halulluka kamar su hakuri da alheri da jimrewa. Kirista wanda ke da wadannan baye-bayen Ruhu darajarsa cikin Ruhu ta fi ta sauran Kirista. Amma ra'ayi na biyu ya rena su baye-bayen, ya kuma mai da su kamar rudi ne kurum. Yin managa da harsuna dabam an mai da shi kamar abin kallo kawai wanda bai sauko daga sama ba ne kuma ba Kirista kadai sukan yi ba. Abu ne na halitta wanda su likitoci masu tone zuciyar dan adam (psychologists), wato masu kimiyya ke nan, suna iya gane da shi. Haka yake da sauran baye-bayen kamar su annabci da warkaswa. Ana iya bayyana su ta hanyar kimiyya, ba tare da zancen RMT ba. Wolters ya cigaba da cewa kafin mu tattauna wadannan ra'ayi guda biyu ya kamata mu san ma'anar "supernatural," kalmar da masu maganar baye-bayen sukan yi amfani da ita kullayaumi. Kalmar ke da ma'ana fiye da daya. Wasu suna nufin abin da bai fita daga halitta ba amma daga sama ko kuwa daga RMT. Ba ya da tushe sam cikin halitta, sai ruhu. Dokokin da Ubangiji ya sa cikin halitta ba su shafe su ba, sai dokokin ruhaniya. Kimiyya ba ta iya ta sa baki ba domin ba na halitta ba ne.**

**Bisa ga ra'ayi na biyu abin da ke supernatural na halitta ne wanda masu kimiyya ke iya bincika, amma ikon Ruhu ya ingantar da abin ko ya gyara abin. Abin yana nan cikin**

**halitta, ba na ruhaniya kadai ba, amma Ruhun ya isantar da shi har sai ka ce sabon abu ne. Ruhun ya gyara abin ya tsarkake shi daga muguntar da tana da iko a kai. Ba bakon abu ba ne a duniya, amma Ruhu ya sabonta shi, ya tsarkake shi. Wolters yana goyon bayan ra'ayi na biyu.**

**To, in ji shi, haka ya ke da baye-bayen Ruhu. Da ma suna nan cikin halitta. Allah ya halicce mu da wasu halulluka kamar kauna, murna da salama, amma zunubi ne ya raba mu da su. Yanzu ta wajen RMT ana iya mayar mana da su, halullukan da da muna da su amma ba cikakke ba, zunubi ne ya bata su, ya rage karfinsu. Ruhu bai kawo mamu wani bakon hali ba ne, amma ya sabonta abin da yana nan tun halittar amma ya lalace.**

**Misalin bangaskiya. Bangaskiya baiwar Ruhu ne (I Kor. 12:7-11), amma KOWANE DAN ADAM YANA DA BANGASKIYA A ZUCIYARSA. Haka Ubangiji ya halicce mu, mu bada gaskiya gareshi. Daga baya muka fadi cikin zunubi, amma har yanzu kowane mutum mai bada gaskiya ne ga wani abu. Im ba bangaskiya ga Ubangiji Allah ba, sai ga wani abu dabam. Wato asalin bangaskiya halitta ne. Ba bakon abu ba ne wajen dan adam. Amma RMT ya sabonta mamu bangaskiyarmu don mu juye zuwa ga Mahalliccinmu mu bada gaskiya gareshi yadda Allah ya nufa tun farko. Aikin RMT ke nan ya gyara abin da yana nan tun farko amma ya lalace. Ruhun ya tsarkake shi. Haka ya faru da bangaskiyarmu. Shi ne yake faruwa da sauran baye-bayen Ruhu. Dukansu za a iske su wajen marasa bi, amma sun lalace, ba a amfani da su yadda Allah ya nufa tun farko.**

**Baye-bayen Ruhu kuwa iri-iri ne. Kowace iyawar da Allah ya isar da dan adam wadda kuma tana karfafa Mulkin Allah da ikiliziyarsa baiwar Ruhu ce. Yin magana cikin harsuna dabam baiwar Ruhu ce mai daraja, amma ana iya bata baiwar. Damuwar Bulus Manzo ke nan. Ana fahariya a kai. Amma haka yake da mutun wanda yana da tunani mai zurfi ko wanda ke "tafiyar da aikin ikiliziya" (I Kor. 12:28), wato da Turanci "administration." To, dai, "administration" aiki ne wanda ake tafiyar makaranta don a koya, amma a nan yana cikin jerin baye-bayen Ruhu tare da annabci da aikata mu'ujizai da dai sauransu. Za ka iya ka koya, amma im ba Ruhu ya sabonta ka ba, ba wuya ka yi amfani da baiwar nan don ka zalunci wadanda ke a hannunka. Ruhu ne zai sabonta ka duk da baiwarka ta administration don ka yi aikin da gaskiya. Ya zama baiwar Ruhu ke nan, amma yana nan tun da. Bataccen halitta ya sadu da Ruhu Mai Gyara. To haka yake da sauran iyawar da dan adam yake da ita, ko aikin makaniki ne ko na karban bako ko na girki ko na shara ko na mulki ko na noma (Ish. 18:23-29). KAN MAGANA A NAN SHI NE WADANNAN BAYE-BAYEN RUHU BA BAKI BA NE CIKIN HALITTAR ALLAH, BA SABOBBIN ABUBUWA BA NE CIKIN DUNIYA. AMMA SUN LALACE, RMT YA SABONTA SU. TA WAJEN HAKA NE SUKA ZAMA BAYE-BAYEN RUHU.**

**Yabo da daukaka su tabatta ga Ubangiji Mahaliccinmu Macecinmu. Amin.**

**CRCN--INA ZA MU?**

**Mai yiwuwa ne wadansu za su dauka kamar na rena baye-bayen da Ruhu ke bayarwa. Sai ka ce na rage masu daraja da shi ke na hada su da duniya da sha'aninta. Me zai hada su? Ba ruhu dabam, duniya dabam ba? Ya kamata mu gane. Da ni da su manyan masu tauhidi na Refom da kuma Majalisa Babba na CRC dukanmu mun yi na'am da baye-bayen RMT. Ana iya aikata su har wa yau. Ko magana cikin harsuna ko warkaswa da sauran ayyukan, ba abin da zai hana a aikata wadannan im ba rashin bangaskiya ba. A nan mun yarda da su Karisimatikai.**

**Inda muke musunsu shi ne dangantakar baiwar Ruhu da halittar Allah. Refom ke cewa baiwar Ruhu baiwa ce wadda tana nan tun farkon halitta. Allah ya nufe mu da su ne. Amma ta wajen zunubi ne su baye-bayen sun lalace. Suna nan amma ba da karfi kamar da ba. Kuma ana moronsu ne domin zalunci da neman girma da dukiya, ba domin ingantar da halittar Allah ko ikiliziyarsa ba. Wadansu Karisimatikai ba su yarda da haka ba domin suna da biyuntaka a zukantansu. Sun rena sha'anin duniya da na jiki cewa Allah bai cika sonsu ba, ba su da daraja wajensa. Wato abin da ke tsakaninmu shi ne biyuntaka. Wanda ya gane da darajar halittar Allah zai iya karbar ra'ayin Refom na game da batun baye-bayen. Wanda ke da biyuntaka a zuciyarsa ba zai iya karba ba domin mun hada sha'anin duniya da na ruhu, abin da su ba swa so ke nan.**

**To, ya yiwu yanzu wadansunka kuna da tambaya a zuciya cewa, "Me wannan likita yake nema yanzu? Ko yana so CRCN ta zama darika iri na Karisimatikai ne? Mu rabu da halinmu na Refom? Ko kuwa da shi ke wasu matsafa suna da wasu iko wandada mu CRCN ba mu da su, mu koma wajen tsafi ko mu shigar da tsafi cikin ikiliziya?" 'Yan'uwa, ba haka ba.**

**Shawara tawa ke nan mu dauki hali na Refom, mu rabu da tsoro. Mu san irin gyaran da ya kamata mu yi da shi ke Refom masu gyara ne. Mu kusanci saurayenmu mu saurare su. Kuma mu saurari masu tauhidi na Refom mu auna abin da zai dace mu yi.**

**Balle mu gane da hanyar da Refom ke auna abubuwan da ke damunsu. Wato a tone su bisa ga**

1. **yadda abin ya ke cikin asalin halitta**
2. **yadda abin ya bata wajen faduwar halitta**
3. **yadda abin ya gyaru da zuwan Yesu ta wurin RMT**

**Wato asirin gyara cikin Refom shi ne mu tone komai bisa**

**ga wannan hanya: HALITTA, FADUWA CIKIN ZUNUBI, CETO KO KUWA GYARA. Shi ne mabudi na gyara cikin ikiliziyar Refom.**

**Har yanzu kuma yawancin lokaci inda damuwa ta tashi ba wuya za a iske BIYUNTAKA a kasa. Refom ba swa son biyuntaka domin biyuntaka reni ne ga abin da Allah ya halitta kuma ya ce yana da kyau. Biyuntaka kuma dalili ne da mu Kirista muka yi ma kanmu cuta a kasar Nijeriya. Cikin zancen baye-bayen ruhu biyuntaka ne ya batar da sha'anin Karisimatikai. Mu dai mu karbi baye-bayen ban da biyuntaka. Mu karbe su bisa ga hanyar gyarar da na jera a sama. Hanyar Refom ke nan.**

**++++++++++++++++**

**LITTATTAFAI**

**Ga wasu takardu inda za a sami karin bayyani na game da kawunan maganganun da aka yi cikin wanna kos din nan.**


**1. HAUSA**

**Boer, J. H. TAFARKIN SALAMA**

**2. TURANCIN KASAR INGILA DA NA KASAR NETHERLANDS**

**Bavinck, H. GEREFORMEERDE DOGMATIEK (Kampen: Bos, 1906).**

**Boer, J. H. WHOLISTIC HEALTH CARE OF, FOR AND BY THE PEOPLE (Lagos and Jos: Christian Health Association of Nigeria, 1989).**

**Boer, J. H. FOUNDATIONS OF BIOMEDICINE (in CHAN's Towards Wholeness, Dec., 1991).**

**Boer, J. H. MISSIONS: HERALDS OF CAPITALISM OR CHRIST? (Ibadan: Daystar Press, 1984).**

**Boer, J. H. CHRISTIANS AND MOBILIZATION (Jos, Institute of Church & Society, 1989).**

**SANARWA: Dukan littattafai masu sunan Boer ana iya samunsu ne a wurinsa (P. O. Box 261, Jos).**

**Broughton, R. S. PARAPSYCHOLOGY: THE CONTROVERSIAL SCIENCE (New York: Ballantine Books, 1991).**

**Brown, T. THE VISION (New York: Berkley Books, 1988).**

**Christian Association of Nigeria. LEADERSHIP IN NIGERIA (Kaduna: CAN, n.d.).**

**Christian Reformed Church. ACTS OF SYNOD, 1973.**

**Davis, H. J. AMERICAN WITCH STORIES (New York: Jonathan David, 1990).**

**Ernest, V. H. I TALKED WITH SPIRITS (Wheaton: Tyndale, 1970).**

**Gersi, D. FACES IN THE SMOKE: AN EYEWITNESS EXPERIENCE OF VOODOO, SHAMANISM, PSYCHIC HEALING AND OTHER AMAZING HUMAN POWERS (Los Angeles: Jeremy P. Tarcher, 1991).**

**Kraft, C. H.  CHRISTIANITY WITH POWER (Ann Arbor: Servant Publications, 1989).**

**Kriel, J. R.  REMOVING MEDICINE'S CARTESIAN MASK (Potchefstroom: Institute for Reformational Studies, 1988).**

**Kuyper, A. and Boer, J. H.  YOU CAN DO GREATER THINGS THAN CHRIST and SCIENCE WITHOUT FAITH IS DEAD (in one binding) (Jos: ICS, 1991).**

**McAlpine, T. H.  FACING THE POWERS (Monrovia, USA: MARC, 1991).**

**Roberts, A. and Donaldson, J.  THE ANTE-NICENE FATHERS. Vol. 4 (Grand Rapids: Eerdmans).**

**Spykman, G. REFORMATIONAL THEOLOGY: A NEW PARADIGM FOR DOING DOGMATICS (Grand Rapids: Eerdmans, 1992).**

**Wolters, A. M.  CREATION REGAINED (Leicester: Intervarsity, 1986).**